الجزء ٢٣ الحزب ٤٥

۞ وَمَآ أَنزَلۡنَا عَلَىٰ قَوۡمِهِۦ مِنۢ بَعۡدِهِۦ مِن جُندٖ مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَمَا
كُنَّا مُنزِلِينَ ٢٨ إِن كَانَتۡ إِلَّا صَيۡحَةٗ وَٰحِدَةٗ فَإِذَا هُمۡ خَٰمِدُونَ
٢٩ يَٰحَسۡرَةً عَلَى ٱلۡعِبَادِۚ مَا يَأۡتِيهِم مِّن رَّسُولٍ إِلَّا كَانُواْ بِهِۦ
يَسۡتَهۡزِءُونَ ٣٠ أَلَمۡ يَرَوۡاْ كَمۡ أَهۡلَكۡنَا قَبۡلَهُم مِّنَ ٱلۡقُرُونِ
أَنَّهُمۡ إِلَيۡهِمۡ لَا يَرۡجِعُونَ ٣١ وَإِن كُلّٞ لَّمَّا جَمِيعٞ لَّدَيۡنَا مُحۡضَرُونَ
٣٢ وَءَايَةٞ لَّهُمُ ٱلۡأَرۡضُ ٱلۡمَيۡتَةُ أَحۡيَيۡنَٰهَا وَأَخۡرَجۡنَا مِنۡهَا حَبّٗا
فَمِنۡهُ يَأۡكُلُونَ ٣٣ وَجَعَلۡنَا فِيهَا جَنَّٰتٖ مِّن نَّخِيلٖ
وَأَعۡنَٰبٖ وَفَجَّرۡنَا فِيهَا مِنَ ٱلۡعُيُونِ ٣٤ لِيَأۡكُلُواْ مِن ثَمَرِهِۦ
وَمَا عَمِلَتۡهُ أَيۡدِيهِمۡۚ أَفَلَا يَشۡكُرُونَ ٣٥ سُبۡحَٰنَ ٱلَّذِي
خَلَقَ ٱلۡأَزۡوَٰجَ كُلَّهَا مِمَّا تُنۢبِتُ ٱلۡأَرۡضُ وَمِنۡ أَنفُسِهِمۡ
وَمِمَّا لَا يَعۡلَمُونَ ٣٦ وَءَايَةٞ لَّهُمُ ٱلَّيۡلُ نَسۡلَخُ مِنۡهُ ٱلنَّهَارَ
فَإِذَا هُم مُّظۡلِمُونَ ٣٧ وَٱلشَّمۡسُ تَجۡرِي لِمُسۡتَقَرّٖ لَّهَاۚ
ذَٰلِكَ تَقۡدِيرُ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡعَلِيمِ ٣٨ وَٱلۡقَمَرَ قَدَّرۡنَٰهُ مَنَازِلَ حَتَّىٰ
عَادَ كَٱلۡعُرۡجُونِ ٱلۡقَدِيمِ ٣٩ لَا ٱلشَّمۡسُ يَنۢبَغِي لَهَآ أَن تُدۡرِكَ
ٱلۡقَمَرَ وَلَا ٱلَّيۡلُ سَابِقُ ٱلنَّهَارِۚ وَكُلّٞ فِي فَلَكٖ يَسۡبَحُونَ ٤٠



**(28) Kuma bamu buqaci mu saukar da rundunar Mala'iku daga sama ba, wajen halakar da mutanensa, waxanda suka qaryata shi, suka kashe shi, lamarinsu a wurin mu ya fi haka sauqi, mun qaddara halakar su ta kasance da tsawa daga sama, ba da saukar da Mala'ikun azaba ba. (29) Qissar halakar da mutanensa ba wata aba ba ce face tsawa guda xaya, da muka aika musu da ita, sai ga su sun faxi a kwance, babu waxanda suka yi saura daga cikinsu. Misalinsu kamar wata wuta ce da take ci, sai ta mutu, ya zama babu abin da ya yi saura daga cikinta. (30) Nadamar bayi masu qaryatawa, da hasarar su ranar alqiyama, yayin da suka ga azaba, domin sun kasance a duniya babu wani Manzo da zai zo musu daga wajen Allah face sai sun yi masa izgili, don haka qarshen su ya zama nadama a ranar alqiyama saboda sakacin da suka yi a cikin haqqin Allah. (31) Waxannan masu qaryatawa da izgili ga Manzanni basu ga abin izina ba ne a cikin al'ummun da suka gabata?. Haqiqa sun mutu, kuma baza su qara dawowa duniya ba, sun tafi zuwa ga abin da suka gabatar na ayyuka, kuma Allah zai musu sakayya a kansu. (32) Duk al'ummu babu makawa sai an halarto da su a gabanmu, ranar alqiyama, babu togaciya, bayan tashinsu bayan mutuwa, don mu saka musu a kan ayyukansu. (33) Alama ga masu qaryata tashi bayan mutuwa ita ce: Wannan qasa busasshiya, mai fari, mun saukar da ruwa daga sama a kanta, sai muka fitar da tsirrai iri –iri a cikinta, da qwayoyi kala-kala don mutane su ci. To, wanda ya raya wannan qasa, ta hanyar saukar mata da ruwa, da fitar da tsirrai, haqiqa shi mai iko ne a kan rayar da matattu bayan sun mutuwa. (34) Muka sanya gonakin dabino da inabi a cikin wannan qasa da muka saukar da ruwa a kanta, muka vuvvugar da inuwan ruwa waxanda suke shayar da ita a cikinta. (35) Don mutane su ci daga 'ya'yan itatuwar waxannan gonaki, daga cikin ni'imar da Allah ya yi musu, ba tare da sun yi wani aiki a cikinsu ba. Yanzu baza su godewa Allah a kan wannan ni'imar ba? Ta hanyar bauta masa shi kaxai, da yin imani da Manzanninsa?. (36) Tsarki ya tabbatar ga Allah, wanda ya fitar da mabambantan tsirrai da bihiyoyi, da kuma rayukan mutane, ya sanya maza da mata, da abin da mutane basu sani ba a cikin halittun Allah, a kan tudu da cikin ruwa da waninsu. (37) Hujja ga mutane a kan kaxaita Allah, ita ce, muna tafiyar da haske ta hanyar tafiyar da yini da kawo dare, a yayin da muke cire yini daga cikinsa, kuma muna zuwa da duhu bayan tafiyar da yini, sai ka ga mutane sun shiga cikin duhu. (38) Alama a gare su da dake nuna kaxaitakar Allah, ita ce wannan rana, wadda take yin gudu, zuwa ga wata matabbatar da Allah ne kaxai ya san yadda take, bata qetare ta. Wannan qaddarawar Mabuwayi ce, wanda babu mai yin galaba a kansa, Masanin da babu abin da yake vuya a gare shi daga al'amarin bayinsa. (39) Wata alama a gare su da take nuna kaxaitakar Allah (S.W.T) ita ce, wannan wata, wanda muka qaddara masa masaukai a kowane dare, yana farawa xan qarami, sannan ya girma, sannan sai ya qanqance, har ya koma kamar nonon dabinon da ya karkace, ya bushe, wajen sirantarsa, da sunkuyawarsa da fatsi fatsinsa da tsufansa. (40) Ayoyin rana, da wata, da dare, da yini, dukkansu suna kan wani tsari ne da Allah ya tsara, basa qetare abin da aka tsara musu. Ba zai yiwu rana ta tarar da wata ba, don ta canja masa hanya, ko ta tafiyar da haskensa, haka ma dare ba zai riga yini ba, ya shigo kafin lokacin yinin ya qare. Dukkan waxannan halittu waxanda aka hore su da waninsu, daga taurari, duk suna da inda suke tafiya a cikinsu a keve, bisa tsarawar Allah da kiyayewarsa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Babu abin da ya fi halitta wulaqanta a wurin Allah idan suka sava masa, kuma babu wanda ya fi su girma idan suka yi masa biyayya.**

**2 - Yana daga hujjoji a kan tashi bayan mutuwa, raya qasa matacciya, ta tsirrar koraye, da fitar da qwaya daga tsiron. 3 - Daga cikin hujjojin kaxaita Allah: halittar halittu a cikin sama da qasa, da tafiyar da su bisa tsari.**

وَءَايَةٞ لَّهُمۡ أَنَّا حَمَلۡنَا ذُرِّيَّتَهُمۡ فِي ٱلۡفُلۡكِ ٱلۡمَشۡحُونِ ٤١ وَخَلَقۡنَا
لَهُم مِّن مِّثۡلِهِۦ مَا يَرۡكَبُونَ ٤٢ وَإِن نَّشَأۡ نُغۡرِقۡهُمۡ فَلَا صَرِيخَ لَهُمۡ
وَلَا هُمۡ يُنقَذُونَ ٤٣ إِلَّا رَحۡمَةٗ مِّنَّا وَمَتَٰعًا إِلَىٰ حِينٖ ٤٤ وَإِذَا
قِيلَ لَهُمُ ٱتَّقُواْ مَا بَيۡنَ أَيۡدِيكُمۡ وَمَا خَلۡفَكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تُرۡحَمُونَ
٤٥ وَمَا تَأۡتِيهِم مِّنۡ ءَايَةٖ مِّنۡ ءَايَٰتِ رَبِّهِمۡ إِلَّا كَانُواْ عَنۡهَا
مُعۡرِضِينَ ٤٦ وَإِذَا قِيلَ لَهُمۡ أَنفِقُواْ مِمَّا رَزَقَكُمُ ٱللَّهُ قَالَ ٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ لِلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَنُطۡعِمُ مَن لَّوۡ يَشَآءُ ٱللَّهُ أَطۡعَمَهُۥٓ إِنۡ
أَنتُمۡ إِلَّا فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ٤٧ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلۡوَعۡدُ إِن كُنتُمۡ
صَٰدِقِينَ ٤٨ مَا يَنظُرُونَ إِلَّا صَيۡحَةٗ وَٰحِدَةٗ تَأۡخُذُهُمۡ وَهُمۡ
يَخِصِّمُونَ ٤٩ فَلَا يَسۡتَطِيعُونَ تَوۡصِيَةٗ وَلَآ إِلَىٰٓ أَهۡلِهِمۡ
يَرۡجِعُونَ ٥٠ وَنُفِخَ فِي ٱلصُّورِ فَإِذَا هُم مِّنَ ٱلۡأَجۡدَاثِ إِلَىٰ رَبِّهِمۡ
يَنسِلُونَ ٥١ قَالُواْ يَٰوَيۡلَنَا مَنۢ بَعَثَنَا مِن مَّرۡقَدِنَاۜۗ هَٰذَا مَا وَعَدَ
ٱلرَّحۡمَٰنُ وَصَدَقَ ٱلۡمُرۡسَلُونَ ٥٢ إِن كَانَتۡ إِلَّا صَيۡحَةٗ
وَٰحِدَةٗ فَإِذَا هُمۡ جَمِيعٞ لَّدَيۡنَا مُحۡضَرُونَ ٥٣ فَٱلۡيَوۡمَ لَا تُظۡلَمُ
نَفۡسٞ شَيۡـٔٗا وَلَا تُجۡزَوۡنَ إِلَّا مَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٥٤



**(41) Alama a gare su a kan kaxaitakar Allah, haka nan ni'imarsa a kan bayinsa ita ce,: Mun xauki waxanda suka kuvuta daga ruwan Xufana, daga cikin zuriyar Annabi Adam, a zamanin Annabi Nuhu, a cikin jirgin ruwa, wanda yake cike da halittun Allah, saboda Allah ya sanya komai a cikin wannan jirgi namiji da mace.**

**(42) Alama a gare su a kan kaxaita Allah da ni'imarsa ga bayinsa ita ce: Mun halitta musu ababen hawa kwatankwacin jirgin Annabi Nuhu.**

**(43) Da mun ga damar nutsar da su, da mun nutsar da su, kuma babu wani mai taimako da zai taimake su, idan muka yi nufin nutsar da su, ko wani mai tseratarwa da zai tseratar da su.**

**(44) Sai dai kawai mun jiqan su, ta hanyar tseratar da su daga nutsewa, da dawo da su, don su ci gaba da jin daxi zuwa wani lokaci qayyadajje, baza su wuce shi ba, ko sa xau izina su yi imani.**

**(45) Idan aka cewa waxannan Mushirikai, masu bijirewa imani: "Ku kiyayi abin da kuke tunkara na lamarin lahira, da wahalhalunta, kuma ku kiyayi duniya, wadda kuke bata baya, da fatan ko Allah zai yi muku baiwar jinqansa, ba za su aikata hakan ba, sai dai su bijire, kuma ba su damu ba.**

**(46) Kuma duk lokacin da ayoyin Allah da suke nuna kaxaitakarsa da cancantarsa da bauta, suka zo wa waxannan mushirikan masu taurin kai, sai su bijire musu, ba su damu da su ba.**

**(47) Idan aka cewa waxannan masu taurin kan: "Ku taimakawa talakawa da miskinai daga dukiyoyin da Allah ya azurta ku da su, sai su mayar, suna masu inkari, su ce: "Yanzu zamu ciyar da waxanda da Allah da ya ga damar ciyar da su, da ya ciyar da su? Ai mu ba zamu savawa abin da Allah ya ga dama ba, ku Muminai ba komai kuke a kai ba, face vata mabayyani da nisa ga barin gaskiya.**

**(48) Kafirai masu inkarin tashi bayan mutuwa, da qaryata shi, masu ganin ba zai yiwu ba, suna cewa: "Yaushe ne za a yi wannan tashin bayan mutuwa, ya ku Muminai, in dai har kuna da gaskiya cikin da'awar zai yi wu?.**

**(49) Waxannan masu qaryata tashi bayan mutuwa, da kore yiwuwar shi ba komai suke jira ba face busa ta farko, yayin da za a yi busa a qaho, sai wannan busa ta shammace su, suna cikin shagulgulan duniya, na saye da sayarwa, da shayarwa da kiwo, da sauran shagulgulan duniya.**

**(50) Yayin da wannan tsawa zata shammacesu, sashensu ba zai iya yi wa sashe wasiyya da komai ba, kuma baza su iya komawa gidajensu da iyalansu ba, zasu mutu ne suna cikin waxannan shagulgulan.**

**(51) Aka yi busa ta biyu a qaho, domin tashi bayan mutuwa, sai ga su gaba xaya suna fitowa daga qaburburansu, zuwa ga Ubangijinsu, suna sauri don yin hisabi da sakamako.**

**(52) Waxannan kafirai masu qaryata tashi bayan mutuwa zasu ce a cikin nadama: "Mun yi asara! Wane ne kuma ya tashe mu daga qaburburan mu?". Sai a amsa musu tambayar su: "Wannan shi ne abin da Allah ya yi alqawarinsa, kuma ba makawa sai ya kasance, Manzanni sun yi gaskiya cikin saqon da suka isar daga Ubangijnsu.**

**(53) Lamarin tashi daga qaburbura bai kasance ba face tasirin busa ta biyu a qaho, sai ka ga dukkan halitta an halarto da su a gare mu ranar alqiyama don yin hisabi. (54) Hukunci zai kasance da adalci a wannan rana, za a zalunce ku – Ya ku bayi - da komai ba, a qara muku munanan ayyukan ku ko a rage muku kyawawan ku. Kaxai ana cika muku sakamakon abin da kua kasance kuna aikatawa a rayuwar duniya.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Daga cikin salon Allah wurin tarbiyyar bayinsa, shi ne ya sanya musu wasu alamomi a gaban su da suke nuna musu abin da zai yi musu amfani a addininsu da duniyar su. 2 - Allah Maxaukakin sarki ya bawa bayinsa karfin da zasu iya aikata da umarni, da nisantar hani. Don haka idan suka bar abin da aka yi musu umarni da shi, to wannan ganin damar su ne.**
**3 - A ranar alqiyama abin da masu imani basu tava zato ba na rahamar Allah zai bayyana a gare su.**

إِنَّ أَصۡحَٰبَ ٱلۡجَنَّةِ ٱلۡيَوۡمَ فِي شُغُلٖ فَٰكِهُونَ ٥٥ هُمۡ وَأَزۡوَٰجُهُمۡ
فِي ظِلَٰلٍ عَلَى ٱلۡأَرَآئِكِ مُتَّكِـُٔونَ ٥٦ لَهُمۡ فِيهَا فَٰكِهَةٞ
وَلَهُم مَّا يَدَّعُونَ ٥٧ سَلَٰمٞ قَوۡلٗا مِّن رَّبّٖ رَّحِيمٖ ٥٨ وَٱمۡتَٰزُواْ
ٱلۡيَوۡمَ أَيُّهَا ٱلۡمُجۡرِمُونَ ٥٩ ۞أَلَمۡ أَعۡهَدۡ إِلَيۡكُمۡ يَٰبَنِيٓ ءَادَمَ (ربع الحزب ٤٥)
أَن لَّا تَعۡبُدُواْ ٱلشَّيۡطَٰنَۖ إِنَّهُۥ لَكُمۡ عَدُوّٞ مُّبِينٞ ٦٠ وَأَنِ
ٱعۡبُدُونِيۚ هَٰذَا صِرَٰطٞ مُّسۡتَقِيمٞ ٦١ وَلَقَدۡ أَضَلَّ مِنكُمۡ
جِبِلّٗا كَثِيرًاۖ أَفَلَمۡ تَكُونُواْ تَعۡقِلُونَ ٦٢ هَٰذِهِۦ جَهَنَّمُ ٱلَّتِي
كُنتُمۡ تُوعَدُونَ ٦٣ ٱصۡلَوۡهَا ٱلۡيَوۡمَ بِمَا كُنتُمۡ تَكۡفُرُونَ ٦٤
ٱلۡيَوۡمَ نَخۡتِمُ عَلَىٰٓ أَفۡوَٰهِهِمۡ وَتُكَلِّمُنَآ أَيۡدِيهِمۡ وَتَشۡهَدُ أَرۡجُلُهُم
بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ٦٥ وَلَوۡ نَشَآءُ لَطَمَسۡنَا عَلَىٰٓ أَعۡيُنِهِمۡ
فَٱسۡتَبَقُواْ ٱلصِّرَٰطَ فَأَنَّىٰ يُبۡصِرُونَ ٦٦ وَلَوۡ نَشَآءُ لَمَسَخۡنَٰهُمۡ
عَلَىٰ مَكَانَتِهِمۡ فَمَا ٱسۡتَطَٰعُواْ مُضِيّٗا وَلَا يَرۡجِعُونَ
٦٧ وَمَن نُّعَمِّرۡهُ نُنَكِّسۡهُ فِي ٱلۡخَلۡقِۚ أَفَلَا يَعۡقِلُونَ ٦٨
وَمَا عَلَّمۡنَٰهُ ٱلشِّعۡرَ وَمَا يَنۢبَغِي لَهُۥٓۚ إِنۡ هُوَ إِلَّا ذِكۡرٞ وَقُرۡءَانٞ مُّبِينٞ
٦٩ لِّيُنذِرَ مَن كَانَ حَيّٗا وَيَحِقَّ ٱلۡقَوۡلُ عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ ٧٠



**(55) Haqiqa 'yan Aljannah a ranar Alqiyama su ababen shagaltarwa ne ga barin yin tunanin wasu, saboda abin da suka gani na ni'ima dauwamammiya, da babban rabo, don haka suna ta farin ciki da walwala. (56) Su da matayensu suna jin daxi a kan gadaje, a qarqashin inuwar Aljannah mai daxi. (57) A cikin wannan Aljannah suna da nau'ika daban daban na 'ya'yan itatuwa, masu daxi, kamar inibi, da vaure, da ruman, kuma suna duk abin da suka nema na jin daxi da kala-kalan ni'ima, duk abin da suka nema za su samu. (58) Qari a kan wannan ni'imar suna da aminci, magana ce daga Ubangiji mai jin qai gare su, idan Allah ya yi musu sallama, sai su samu aminci ta kowane vangare, kuma sun samu gaisuwar da ba ta sama da ita. (59) Za a cewa Mushirikai ranar alqiyama a ce: "Ku ware daga cikin Muminai, bai dace da su ba, su zama tare da ku, saboda a kwai bambanci a tsakanin sakamakon ku da sakamakon su, da siffofin ku da siffofinsu.**

**(60) Ashe ban yi muku wasiyya da umarni ba, a kan harshen Manzanni na, na ce da ku: "Ya ku 'ya'yan Adam, kada ku bi Shaixan, ta hanyar aikata kafirci kala-kala da savo. Haqiqa Shaixan maqiyinku ne, mai bayyana adawa, to ta yaya mai hankali zai yi bi maqiyinsa, wanda adawarsa ta bayyana?!. (61) Kuma na umarce ku – Ya ku 'ya'yan Adam - ku bauta mini ni kaxai, kada ku haxa ni da kowa a wurin bauta. Bauta min ni kaxai da yi min xa'a ita ce, hanya miqaqqiya, da take kaiwa zuwa ga samun yarda ta, da shiga Aljannah. Sai dai baku yi abin da na yi muku wasiyya, kuma na umarce ku da shi ba. (62) Haqiqa Shaixan ya vatar da halitta mai yawa daga cikinku, shin baku da hankali ne, da zai umarce ku da yi wa Ubangijinku xa'a, da bauta masa shi kaxai, kuma ya hana ku yi wa shaixan xa'a, wanda yake maqiyinku ne, mai bayyana adawa a gare ku?!. (63) Wannan ita ce Jahannama wadda ake yi muku alqawarinta a duniya saboda kafircinku, kuma a lokacin gaibu ce, amma a yau ga ta kuna ganinta ido biyu. (64) Ku shige ta a yau, ku wahala da zafinta, saboda kafirce wa Allah da kuka yi a rayuwarku ta duniya.**

**(65) A yau zamu rufe bakunansu, sai su zama bebaye, basa iya yin inkarin abin da suke kai na kafirci da savo. Sai hannayensu su yi mana magana da abin da suka aikata a duniya, qafafuwansu su bada shaida a kan abin da suka aikata na savo, suka tafi zuwa gare shi. (66) Da mun ga damar tafiyar da ganinsu, da mun tafiyar da shi, baza su ga komai ba, sai kaga suna rigeggeniya zuwa ga siraxi, domin su wuce zuwa Aljannah, amma ba zai yiwu ba su tsallake, tunda basa gani. (67) Da mun ga damar canza musu halittarsu, da zaunar da su a kan qafafuwansu, da mun canza halittarsu, mun zaunar da su a kan qafafunsu, ba zasu iya barin inda suke ba, kuma ba zasu iya tafiya gaba ba, haka ma ba zasu iya dawowa baya ba. (68) Duk wanda a cikin mutane muka ja kwanansa, ta hanyar tsawaita rayuwarsa, to zamu komar da shi ga mataki na rauni, shin basa tunani da hankulan su ne? su gane cewa wannan gidan ba gidan dauwama ba ne, gidan dauwama shi ne gidan lahira. (69) Ba mu koyawa Annabi Muhammad (S.W.A) waqa ba, kuma hakan bai dace da shi ba, domin ba xabi'arsa ba ce, kuma a halittarsa ma ba zai iya ba, ballantana har ya inganta ku ce masa mawaqi ne. Ba komai muka koya masa ba sai zikiri da Alqur'ani, kuma hakan a bayyane yake ga wanda ya lura da shi. (70) Don ya gargaxi wanda zuciyarsa take rayayya, mai basira, wannan shi yake amfana da shi. Azaba kuma ta tabbata a kan kafirai, saboda hujja ta tsaya a kansu, da saukar da Alqur'ani, da isar da'awarsa zuwa gare su, don haka basu da wani uzuri da za su faxa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yan Aljannah zasu kasance masu farin ciki da dukkan abin da zukata suke so, idanuwa suke jin daxi da su, masu buri suke burinsu. 2 - Mai zuciya shi ne wanda yake tsarkaka da Alqur'ani, kuma yake qara ilimi da shi da aiki. 3 - Gavvan xan Adam zasu yi masa shaida ranar alqiyama.**

أَوَلَمۡ يَرَوۡاْ أَنَّا خَلَقۡنَا لَهُم مِّمَّا عَمِلَتۡ أَيۡدِينَآ أَنۡعَٰمٗا فَهُمۡ لَهَا
مَٰلِكُونَ ٧١ وَذَلَّلۡنَٰهَا لَهُمۡ فَمِنۡهَا رَكُوبُهُمۡ وَمِنۡهَا يَأۡكُلُونَ
٧٢ وَلَهُمۡ فِيهَا مَنَٰفِعُ وَمَشَارِبُۚ أَفَلَا يَشۡكُرُونَ ٧٣ وَٱتَّخَذُواْ
مِن دُونِ ٱللَّهِ ءَالِهَةٗ لَّعَلَّهُمۡ يُنصَرُونَ ٧٤ لَا يَسۡتَطِيعُونَ
نَصۡرَهُمۡ وَهُمۡ لَهُمۡ جُندٞ مُّحۡضَرُونَ ٧٥ فَلَا يَحۡزُنكَ قَوۡلُهُمۡۘ
إِنَّا نَعۡلَمُ مَا يُسِرُّونَ وَمَا يُعۡلِنُونَ ٧٦ أَوَلَمۡ يَرَ ٱلۡإِنسَٰنُ أَنَّا
خَلَقۡنَٰهُ مِن نُّطۡفَةٖ فَإِذَا هُوَ خَصِيمٞ مُّبِينٞ ٧٧ وَضَرَبَ لَنَا
مَثَلٗا وَنَسِيَ خَلۡقَهُۥۖ قَالَ مَن يُحۡيِ ٱلۡعِظَٰمَ وَهِيَ رَمِيمٞ ٧٨
قُلۡ يُحۡيِيهَا ٱلَّذِيٓ أَنشَأَهَآ أَوَّلَ مَرَّةٖۖ وَهُوَ بِكُلِّ خَلۡقٍ عَلِيمٌ
٧٩ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُم مِّنَ ٱلشَّجَرِ ٱلۡأَخۡضَرِ نَارٗا فَإِذَآ أَنتُم
مِّنۡهُ تُوقِدُونَ ٨٠ أَوَلَيۡسَ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ
بِقَٰدِرٍ عَلَىٰٓ أَن يَخۡلُقَ مِثۡلَهُمۚ بَلَىٰ وَهُوَ ٱلۡخَلَّٰقُ ٱلۡعَلِيمُ ٨١
إِنَّمَآ أَمۡرُهُۥٓ إِذَآ أَرَادَ شَيۡـًٔا أَن يَقُولَ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ٨٢
فَسُبۡحَٰنَ ٱلَّذِي بِيَدِهِۦ مَلَكُوتُ كُلِّ شَيۡءٖ وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ٨٣

آياتها ١٨٢ — سُورَةُ الصَّافَّاتِ — ترتيبها ٣٧



**(71) Shin basu gani ba ne, Mun halitta musu dabbobin ni'ima, kuma muka sanya su masu mallakar al'amuran waxannan dabbobi, suna sarrafa su cikin abin da maslahar su take ciki.**

**(72) Mun hore musu waxannan dabbobin, mun sanya su masu jayuwa zuwa gare su, su na hawa bayan wasu daga cikinsu, suna xora musu kayansu, kuma suna cin naman wasu daga cikinsu. (73) Suna da wasu amfanin bayan hawa da cin namansu, kamar amfani da fatun su, da gashin su, da kitsensu da kuxin su. kuma daga gare su ne suke sana'anta shimfixu da tufafi, kuma suna da abin sha daga gare su, suna shan nonon su. Yanzu ba zasu godewa Allah, wanda ya yi musu wannan ni'imar da waninta ba?.**

**(74) Mushirikai sun riqi wasu ababen bautar ba Allah ba suna bauta musu, da fatan zasu taimaka musu, su tseratar da su daga azabar Allah.**

**(75) Waxannan ababen bautar da suka riqa, ba zasu iya taimakon kansu da komai ba, ko taimakon waxanda suke bauta musu koma bayan Allah, su da gumakansu duk sai an zo da su cikin azabar Allah, kowa yana barranta daga xan uwansa. (76) Ya kai wannan Manzo, kada cewar su: "Kai ba Manzo ba ne, ko kai mawaqi ne, ko abin da ya yi kama da haka cikin sharrinsu ya baqanta maka rai. Haqiqa mun san abin da suke voyewa daga cikin haka, da wanda abin da suke bayyanawa, babu abin da yake vuya a gare mu, kuma zamu saka musu a kansu.**

**(77) Mutumin da yake inkarin tashi bayan mutuwa, baya tunanin mun halicce shi daga maniyyi, sannan ya wuce ta matakai daban daban har aka haife shi, ya taso, kuma ya zama mai yawan husuma da jidali, yanzu bai kalli wannan ba, don ya gane yiwuwar tashi bayan mutuwa ba?.**

**(78) Wannan kafiri ya rafkana, kuma ya yi jahilci, da har yake kafa hujja da rididdigaggen qashi a kan rashin yiwuwar tashi bayan mutuwa, yake cewa: "Wa ye zai dawo da wannan qashi? Amma ya manta halittarsa daga babu. (79) Ka fada - Ya kai wannan Manzo, kana mai ba shi amsa: "Waxannan qasusuwa da suka rididdige, wanda ya fara halittarsu da farko shi ne zai raya su, kuma wanda ya yi halicce su da farko ai ba zai kasa dawo da rayuwa a gare su ba, kuma shi Allah Maxaukakin sarki Masani ne a kan kowace halitta, babu abin da yake vuya a gare shi.**

**(80) Wanda ya sanya muku wuta daga bishiyar da take koriya, xanya, kuke fitar da ita daga wannan bishiya, kuke kunna wuta daga gare ta. To wanda ya haxa tsakanin kishiyoyi guda biyu - tsakanin xanyartakar ruwan koriyar bishiya, da kuma wuta mai ci a cikinta – wanda duk ya yi haka to mai iko ne a kan raya matattu.**

**(81) Shin wanda ya halicci sammai da qassai, tare da abin da yake cikinsu mai girma, ba mai iko ba ne a kan raya matattu bayan mutuwarsu ba? Haka ne, Shi mai iko ne a kan hakan, kuma shi ne mai yawan halitta, wanda ya halicci dukkan halittu, kuma masanin su, babu abin da yake vuya a gare shi game da su. (82) Kaxai lamarin Allah da sha'aninsa Maxaukakin sarki, idan ya yi nufin samar da wani abu, to kawai zai ce masa: "Kasance". Sai wannan abin da yake son ya kasance, daga cikin abin da yake so akwai raya matattu, da kashewa da tashi bayan mutuwa, da sauransu. (83) Allah ya tsarkaka, kuma ya girmama, daga abin da Mushirikai suke danganta masa na gajiyawa, kuma shi ne yake mallakar dukkan abubuwa, yana sarrafa su yadda ya ga dama, kuma a hannunsa ne mabuxan dukkan komai suke, kuma gare shi, shi kaxai za a komar da ku a lahira, ya saka muku a kan ayyukanku.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Yana daga falalar Allah da ni'imarsa a kan mutane, hore musu dabbobi, domin amfanin daban daban. 2 - Yawan hujjoji na hankali a kan ranar alqiyama da bijirewar mushirikai ga hakan. 3 - Yana daga siffofin Allah iliminsa ya game duk halittarsa, a kowane hali da lokaci, kuma ya san abin da qasa take ci daga jikin matattu da abin da ya yi saura, kuma ya san abin da yake voye (Gaibu) da abin da yake bayyane.**

# Suratus Saffat

An Saukar Da Ita A Makkah

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ
وَالصَّافَّاتِ صَفًّا ﴿١﴾ فَالزَّاجِرَاتِ زَجْرًا ﴿٢﴾ فَالتَّالِيَاتِ ذِكْرًا ﴿٣﴾ إِنَّ
إِلَٰهَكُمْ لَوَاحِدٌ ﴿٤﴾ رَبُّ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا وَرَبُّ
الْمَشَارِقِ ﴿٥﴾ إِنَّا زَيَّنَّا السَّمَاءَ الدُّنْيَا بِزِينَةٍ الْكَوَاكِبِ ﴿٦﴾ وَحِفْظًا
مِنْ كُلِّ شَيْطَانٍ مَارِدٍ ﴿٧﴾ لَا يَسَّمَّعُونَ إِلَى الْمَلَإِ الْأَعْلَىٰ وَيُقْذَفُونَ
مِنْ كُلِّ جَانِبٍ ﴿٨﴾ دُحُورًا وَلَهُمْ عَذَابٌ وَاصِبٌ ﴿٩﴾ إِلَّا مَنْ خَطِفَ
الْخَطْفَةَ فَأَتْبَعَهُ شِهَابٌ ثَاقِبٌ ﴿١٠﴾ فَاسْتَفْتِهِمْ أَهُمْ أَشَدُّ خَلْقًا أَمْ
مَنْ خَلَقْنَا إِنَّا خَلَقْنَاهُمْ مِنْ طِينٍ لَازِبٍ ﴿١١﴾ بَلْ عَجِبْتَ وَيَسْخَرُونَ
﴿١٢﴾ وَإِذَا ذُكِّرُوا لَا يَذْكُرُونَ ﴿١٣﴾ وَإِذَا رَأَوْا آيَةً يَسْتَسْخِرُونَ ﴿١٤﴾
وَقَالُوا إِنْ هَٰذَا إِلَّا سِحْرٌ مُبِينٌ ﴿١٥﴾ أَإِذَا مِتْنَا وَكُنَّا تُرَابًا وَعِظَامًا
أَإِنَّا لَمَبْعُوثُونَ ﴿١٦﴾ أَوَآبَاؤُنَا الْأَوَّلُونَ ﴿١٧﴾ قُلْ نَعَمْ وَأَنْتُمْ دَاخِرُونَ
﴿١٨﴾ فَإِنَّمَا هِيَ زَجْرَةٌ وَاحِدَةٌ فَإِذَا هُمْ يَنْظُرُونَ ﴿١٩﴾ وَقَالُوا يَا وَيْلَنَا
هَٰذَا يَوْمُ الدِّينِ ﴿٢٠﴾ هَٰذَا يَوْمُ الْفَصْلِ الَّذِي كُنْتُمْ بِهِ تُكَذِّبُونَ ﴿٢١﴾
الحزب ٤٥ ۞ احْشُرُوا الَّذِينَ ظَلَمُوا وَأَزْوَاجَهُمْ وَمَا كَانُوا يَعْبُدُونَ ﴿٢٢﴾ مِنْ دُونِ
اللَّهِ فَاهْدُوهُمْ إِلَىٰ صِرَاطِ الْجَحِيمِ ﴿٢٣﴾ وَقِفُوهُمْ إِنَّهُمْ مَسْئُولُونَ ﴿٢٤﴾

**Daga Manufofin Surar:** **Tsarkake Allah daga abin da mushrikai suka jingina masa, da vata abin da suke riyawa a kan Mala'iku da Aljanu.**

**Tafsir:** **(1) Allah ya rantse da Mala'iku waxanda suke yin sahu yayin ibadar su a jejjere. (2) Kuma ya rantse da Mala'iku masu yin tsawa ga girgije, su kora shi zuwa ga inda Allah ya ga dama ya saukar da ruwa. (3) Kuma ya rantse da Mala'ikun da su ke karanta maganar Allah. (4) Tabbas abin bautawar ku na gaskiya - Ya ku mutane - guda xaya ne, ba shi da abokin tarayya, shi ne Allah. (5) Ubangijin Sammai, kuma Ubangijin Qassai, Ubangijin abin da yake tsakaninsu, Ubangijin rana wajen vullowarta da faxuwarta a tsawon shekara. (6) Haqiqa mun qawata sama mafi kusaci da qasa da ado mai kyau, shi ne taurari, waxanda idan ka kalle su tamkar wasu abubuwa masu tsada masu qyalqyali. (7) Muka kiyaye sama ta duniya da taurari, daga dukkan wani shaixan mai taurin kai, mai fita daga xa'ar Allah, sai a jefe shi da su. (8) Waxannan shaixanu basa iya sauraron Mala'iku a sama, idan Mala'iku suka yi magana da junansu a kan wahayin da Ubangijinsu ya yi musu na shari'arsa, ko abin da ya tsara, ana jifar su da tauraro mai wuta ta kowane vangare. (9) Don a kore su a nisanta su ga barin sauraronsu, kuma a lahira suna da azaba mai raxaxi, dauwamammiya wadda bata yankewa. (10) Sai wanda ya fizgi wani abu daga cikin shaixanun, kalma guda xaya daga cikin abin da Mala'iku suke tattaunawa a tsakaninsu, wanda mutanen qasa ba su sani ba, to sai tauraro mai walqiya ya bi shi, ya qona shi, to ta yiwu ya isar da wannan kalmar zuwa ga 'yan uwansa, har ta isa wurin bokaye gabanin tauraron ya qone shi, sai su haxa qarya xari tare da ita. (11) Ya Muhammad, ka tambayi kafirai masu inkarin tashi bayan mutuwa: "Shin su suka fi wahalar halitta, da qarfin jiki, da girman gavvai, fiye da abin da muka halitta na sammai da qassai da Mala'iku?. Lallai mun halicce su daga tavo me danqo. to ta yaya zasu riqa inkarin tashi bayan mutuwa? alhali su ababen halitta ne daga abu mai rauni, shi ne tavo mai danqo?. (12) Ka yi mamakin ikon Allah da tsarinsa ga sha'anin halittarsa, kuma ka yi mamakin qaryatawar mushrikai ga tashi bayan mutuwa. Waxannan mushrikai saboda tsabar qaryatawar su ga tashi bayan mutuwa, suna yin izgili a kan abin da kake faxa a kan hakan. (13) Idan aka yi wa waxannan mushrikai wa'azi, basa wa'azantuwa da wa'azin, ba sa amfanuwa, saboda abin da suke kai na qeqashewar zuciya. (14) Kuma idan suka ga wata aya daga cikin ayoyin Annabi (S.A.W) da suke nuna gaskiyarsa, sai su kai matuqa wajen izgili da mamakin ta. (15) Suka ce: "Abin da Annabi Muhammad ya zo da shi, ba komai ba ne illa tsafi mabayyani". (16) "A ce wai yanzu idan muka mutu, muka zama turvaya da qasusuwa rididdigaggu, wai za a tashe mu rayayyu bayan haka?. Wannan abu ne ba mai yiwuwa ba". (17) "Ko a ce za a tashi iyayenmu na farko, waxanda suka mutu gabanin mu?". (18) Ka gaya musu - Ya kai Muhammad - kana mai basu amsa: "Tabbas za a tashe ku bayan kun zama turvaya, rididdigaggun qasusuwa, kuma a tada iyayenku na farko, za a tashe ku gaba xaya, kuna cikin qasqanci da wulaqanci. (19) Kaxai dai busa ce guda xaya da za a yi a qaho (busa ta biyu) sai ka gan su dukkansu suna kallon tashin hankalin ranar alqiyama, suna jiran me Allah zai yi musu. (20) Mushirikai masu qaryata tashi bayan mutuwa suka ce: "Mun halaka, wannan ita ce ranar sakamako, ranar da Allah yake sakawa bayinsa a kan abin da suka gabatar a rayuwarsu ta duniya na ayyuka". (21) Sai a ce da su: "Yau ranar hukunci ce a tsakanin bayi, wadda kuka kasance kuna inkarinta da qaryatawa da ita a duniya". (22) (23) Za a cewa Mala'iku a wannan rana: "Ku tara mushirikai azzalumai saboda shirkarsu, su da makamantansu a yin shirka, da masu goya musu baya akan qaryatawa, da abin da suka kasance suna bautawa koma bayan Allah na gumaka, ku nuna musu hanyar shiga wuta, ku nuna musu ita, ku kora su gare ta, ita ce makomarsu. (24) Kuma ku tsare su kafin a shigar da su wuta, don a yi musu hisabi, su ababen tambaya ne, sannan bayan haka sai ku kora su zuwa ga wutar.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - An qawata sama ta duniya ne da taurari don wasu amfani, daga cikinsu akwai: samar da ado, da samar da tsaro daga kangararren shaixan. 2 - Tabbatar da siraxi, wanda wata gada ce da aka gindaya ta a kan wutar Jahannama, 'yan Aljannah zasu qetare ta, qafar 'yan wuta kuma zata zame daga kansa.**

مَا لَكُمۡ لَا تَنَاصَرُونَ ٢٥ بَلۡ هُمُ ٱلۡيَوۡمَ مُسۡتَسۡلِمُونَ ٢٦ وَأَقۡبَلَ بَعۡضُهُمۡ
عَلَىٰ بَعۡضٖ يَتَسَآءَلُونَ ٢٧ قَالُوٓاْ إِنَّكُمۡ كُنتُمۡ تَأۡتُونَنَا عَنِ ٱلۡيَمِينِ ٢٨
قَالُواْ بَل لَّمۡ تَكُونُواْ مُؤۡمِنِينَ ٢٩ وَمَا كَانَ لَنَا عَلَيۡكُم مِّن سُلۡطَٰنِۭۖ
بَلۡ كُنتُمۡ قَوۡمٗا طَٰغِينَ ٣٠ فَحَقَّ عَلَيۡنَا قَوۡلُ رَبِّنَآۖ إِنَّا لَذَآئِقُونَ ٣١
فَأَغۡوَيۡنَٰكُمۡ إِنَّا كُنَّا غَٰوِينَ ٣٢ فَإِنَّهُمۡ يَوۡمَئِذٖ فِي ٱلۡعَذَابِ مُشۡتَرِكُونَ
٣٣ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَفۡعَلُ بِٱلۡمُجۡرِمِينَ ٣٤ إِنَّهُمۡ كَانُوٓاْ إِذَا قِيلَ لَهُمۡ
لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ يَسۡتَكۡبِرُونَ ٣٥ وَيَقُولُونَ أَئِنَّا لَتَارِكُوٓاْ ءَالِهَتِنَا
لِشَاعِرٖ مَّجۡنُونِۭ ٣٦ بَلۡ جَآءَ بِٱلۡحَقِّ وَصَدَّقَ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ٣٧ إِنَّكُمۡ
لَذَآئِقُواْ ٱلۡعَذَابِ ٱلۡأَلِيمِ ٣٨ وَمَا تُجۡزَوۡنَ إِلَّا مَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ
٣٩ إِلَّا عِبَادَ ٱللَّهِ ٱلۡمُخۡلَصِينَ ٤٠ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ رِزۡقٞ مَّعۡلُومٞ ٤١
فَوَٰكِهُ وَهُم مُّكۡرَمُونَ ٤٢ فِي جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ٤٣ عَلَىٰ سُرُرٖ مُّتَقَٰبِلِينَ
٤٤ يُطَافُ عَلَيۡهِم بِكَأۡسٖ مِّن مَّعِينِۭ ٤٥ بَيۡضَآءَ لَذَّةٖ لِّلشَّٰرِبِينَ
٤٦ لَا فِيهَا غَوۡلٞ وَلَا هُمۡ عَنۡهَا يُنزَفُونَ ٤٧ وَعِندَهُمۡ قَٰصِرَٰتُ
ٱلطَّرۡفِ عِينٞ ٤٨ كَأَنَّهُنَّ بَيۡضٞ مَّكۡنُونٞ ٤٩ فَأَقۡبَلَ بَعۡضُهُمۡ عَلَىٰ
بَعۡضٖ يَتَسَآءَلُونَ ٥٠ قَالَ قَآئِلٞ مِّنۡهُمۡ إِنِّي كَانَ لِي قَرِينٞ ٥١



**(25) Za a ce musu cikin tozartawa: "Me yasa sashinku basa taimakon sashi, kamar yadda kuka kasance kuna taimakon juna a duniya, kuma kuke riya cewa gumakan ku za su taimake ku?". (26) Kawai dai su a yau masu jayuwa ne ga lamarin Allah, cikin qasqanci, sashensu baya taimakon sashe, saboda gazawa da qarancin dabararsu. (27) Sai sashinsu ya juyo ga sashi, suna zargin juna, suna husuma, a lokacin da zargin juna, da yin husuma ba su da wani amfani. (28) Sai mabiya suka cewa waxanda suke bi: "Haqiqa ku – Manyanmu - kun kasance kuna zuwa mana ta vangaren addini da gaskiya, sai ku qawata mana kafirci da shirka da Allah, da aikata savo, kuma qyamatar da mu gaskiya, wadda Manzanni suka zo da ita daga wurin Allah. (29) Sai waxanda aka bi su cewa mabiyansu: "Lamarin ba kamar yadda kuka riya ba ne, dama can kun kasance a kan kafirci, baku tava zama muminai ba, kai! Kun ma kasance masu yin inkari". (30) "Kuma ba mu da wani iko a kanku - Ya ku mabiya – na qarfi ko rinjaye ballantana mu jefa ku cikin kafirci da shirka da aikata savo, kawai dai ku, kun kasance mutane masu qetare iyaka a cikin kafirci da vata". (31) Don haka alqawarin Allah na azaba ya tabbata a kanmu baki xaya, inda ya ce: (Tabbas zan cika wutar Jahannama da kai – Shaixan - da waxanda suka bi ka daga cikinsu gaba xaya). [saad: 85] don haka ba makawa sai mun xanxani abin da Ubangijinmu ya yi alqawari". (32) Muka kirawo ku zuwa ga vata da kafirci, haqiqa dama mun kasance vatattu ga barin tafarkin shiriya. (33) Don haka mabiya da waxanda aka bi a ranar alqiyama duk za su yi tarayya a cikin azaba. (34) Haqiqa mu kamar yadda muka xanxana wa waxannan azaba, haka muke aikatawa masu laifi daga waninsu. (35) Haqiqa waxannan mushrikai idan aka ce da su a duniya: "La Ilaha Illal Lahu", don su yi aiki da abin da ta qunsa, da barin abin da ya sava mata, sai su qi amsawa da miqa wuya, don girman kai ga gaskiya. (36) Suna cewa, suna masu kafa hujja a kan kafircinsu: "kawai zamu bar bautar gumakan mu, saboda wani mawaqi mahaukaci? Suna nufin Manzon Allah (S.A.W) da wannan magana. (37) Haqiqa sun qirqiri babbar qarya, Manzon Allah bai kasance mahaukaci ko mawaqi ba. Tabbas ya zo da Alqur'ani mai kira zuwa ga kaxaita Allah, da bin Manzonsa, kuma ya gasgata Manzanni cikin abin da suka zo da shi daga Allah na kaxaita shi, da tabbatar da dawowa, kuma bai sava musu da komai ba. (38) Tabbas ku – Mushrikai - masu xanxanar azaba ce mai ciwo a ranar alqiyama, saboda kafircinku da qaryata Manzanni. (39) Ba a saka muku – Ya ku Mushirika – da komai face abin da kuka kasance kuna aikata wa a duniya na kafirci da Allah da aikata savo. (40) Sai dai bayin Allah Muminai da Allah ya tsarkake su don bauta masa, su ma suka tsarkake shi da bauta, tabbas su za su tsira daga azaba. (41) Waxancan bayi masu tsarkake Allah, suna da wani arziki da Allah zai azurta su da shi, wanda yake sannane a wajen daxinsa da kyansa da dauwamarsa. (42) Yana daga cikin wannan arziki, za a azurta su da kayan marmari mafi daxi da za su riqa ci da marmari, kuma qari a kan haka su ababen gimamawa ne ta hanyar xaukaka matsayinsu, da ba su damar kallon fuskar Allah mai girma. (43) Duk wannan za su same shi ne a cikin Aljannatai na ni'ima madauwamiya, wadda ba ta yankewa. (44) Suna kashingixe a kan gadaje na alfarma, suna fuskantar juna, sashensu yana kallon sashe. (45) Ana kewaya su da kofunan giya, wadda take kamar ruwa mai gudana wajen garai-garai. (46) Fara fat, mai shanta yana jin daxi cikakke idan ya sha ta. (47) Kuma ba kamar giyar duniya ba ce, a cikinta babu abin da yake tafiyar da hankali na maye, haka nan ciwon kai baya kama mai shanta, hankalin mai shan ta da jikinsa suna zama qalau. (48) Kuma a cikin Aljannah suna da kamammun mataye, waxanda idanuwansu basa kallon waxanda ba mazajensu ba, kuma masu kyawawan idanu. (49) Saboda kyan launinsu wanda ya haxu da kala mai kyau kai ka ce qwai ne wanda aka tsare shi, hannu bai tava shafar sa ba. (50) Sai sashen 'yan Aljannah ya fuskanci sashe, suna tambayar juna a kan abin da ya wuce da abin da ya faru da su a duniya. (51) Sai wani daga cikin Muminai ya ce: "Haqiqa ni, ina da wani aboki a duniya, wanda yake musun tashi bayan mutuwa".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Sababin azabtar da kafirai shi ne, mummunan aiki, wato shirka da savon Allah.**

**2 - Yana daga ni'imar 'yan-Aljannah haxuwar sashen da sashe, da ganawar sashe da sashe, wanda hakan yana cikin cikar farin ciki.**

يَقُولُ أَءِنَّكَ لَمِنَ ٱلْمُصَدِّقِينَ ﴿٥٢﴾ أَءِذَا مِتْنَا وَكُنَّا تُرَابًا وَعِظَـٰمًا أَءِنَّا
لَمَدِينُونَ ﴿٥٣﴾ قَالَ هَلْ أَنتُم مُّطَّلِعُونَ ﴿٥٤﴾ فَٱطَّلَعَ فَرَءَاهُ فِى سَوَآءِ
ٱلْجَحِيمِ ﴿٥٥﴾ قَالَ تَٱللَّهِ إِن كِدتَّ لَتُرْدِينِ ﴿٥٦﴾ وَلَوْلَا نِعْمَةُ رَبِّى
لَكُنتُ مِنَ ٱلْمُحْضَرِينَ ﴿٥٧﴾ أَفَمَا نَحْنُ بِمَيِّتِينَ ﴿٥٨﴾ إِلَّا مَوْتَتَنَا
ٱلْأُولَىٰ وَمَا نَحْنُ بِمُعَذَّبِينَ ﴿٥٩﴾ إِنَّ هَـٰذَا لَهُوَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿٦٠﴾
لِمِثْلِ هَـٰذَا فَلْيَعْمَلِ ٱلْعَـٰمِلُونَ ﴿٦١﴾ أَذَٰلِكَ خَيْرٌ نُّزُلًا أَمْ شَجَرَةُ
ٱلزَّقُّومِ ﴿٦٢﴾ إِنَّا جَعَلْنَـٰهَا فِتْنَةً لِّلظَّـٰلِمِينَ ﴿٦٣﴾ إِنَّهَا شَجَرَةٌ
تَخْرُجُ فِىٓ أَصْلِ ٱلْجَحِيمِ ﴿٦٤﴾ طَلْعُهَا كَأَنَّهُۥ رُءُوسُ ٱلشَّيَـٰطِينِ
﴿٦٥﴾ فَإِنَّهُمْ لَـَٔاكِلُونَ مِنْهَا فَمَالِـُٔونَ مِنْهَا ٱلْبُطُونَ ﴿٦٦﴾ ثُمَّ إِنَّ لَهُمْ
عَلَيْهَا لَشَوْبًا مِّنْ حَمِيمٍ ﴿٦٧﴾ ثُمَّ إِنَّ مَرْجِعَهُمْ لَإِلَى ٱلْجَحِيمِ ﴿٦٨﴾
إِنَّهُمْ أَلْفَوْا۟ ءَابَآءَهُمْ ضَآلِّينَ ﴿٦٩﴾ فَهُمْ عَلَىٰٓ ءَاثَـٰرِهِمْ يُهْرَعُونَ ﴿٧٠﴾
وَلَقَدْ ضَلَّ قَبْلَهُمْ أَكْثَرُ ٱلْأَوَّلِينَ ﴿٧١﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا فِيهِم
مُّنذِرِينَ ﴿٧٢﴾ فَٱنظُرْ كَيْفَ كَانَ عَـٰقِبَةُ ٱلْمُنذَرِينَ ﴿٧٣﴾
إِلَّا عِبَادَ ٱللَّهِ ٱلْمُخْلَصِينَ ﴿٧٤﴾ وَلَقَدْ نَادَىٰنَا نُوحٌ فَلَنِعْمَ
ٱلْمُجِيبُونَ ﴿٧٥﴾ وَنَجَّيْنَـٰهُ وَأَهْلَهُۥ مِنَ ٱلْكَرْبِ ٱلْعَظِيمِ ﴿٧٦﴾



**(52) Yana fada min cikin inkari da izgili: “Shin wai kai abokina kana cikin waxanda suka gasgata da tayar da matattu?”. (53) Yanzu a ce bayan mun mutu, mun zama turvaya da qasusuwa lalatattu, wai za a tashe mu, kuma a yi mana sakayya a kan ayyukan da muka aikata a duniya?”. (54) Sai Muminin abokinsa ya cewa abokansa ‘yan Aljannah: “Ku zo mu leqa don mu ga makomar wancan abokin nawa, wanda yake inkarin tashi bayan mutuwa”. (55) Sai ya ya leqa, kawai sai ya ga abokin nasa a tsakiyar wutar Jahannama.**

**(56) Sai ya ce: “Na rantse da Allah ka kusa ka halakar da ni, ka janyo min shiga wuta, ta hanyar kira na zuwa ga kafirci, da inkarin tashi bayan mutuwa”. (57) “Ba don Allah ya yi min baiwa da shiriya zuwa ga imani ba, kuma ya datar da ni zuwa gare shi, da ni ma na zama kamarka, cikin waxanda za a halarto da shi a yi masa azaba kamar kai”. Yayin da ya gama magana da abokinsa daga cikin ‘yan wuta, sai ya fuskantar da maganarsa zuwa ga abokansa ‘yan Aljannah ya ce: (58) “Mu ‘yan-Aljannah ba masu mutuwa ba ne”.**

**(59) Sai dai mutuwar da muka yi ta farko a duniya, za a dauwamar da mu cikin Aljannah ne, kuma baza a azabtar da mu ba, kamar yadda ake azabtar da kafirai. (60) Tabbas wannan sakamakon da ubangijinmu ya yi mana, na shiga Aljannah, da dauwama a cikinta, da kuvuta daga wuta, lallai shi ne samun rabo mai girma, wanda babu rabon da ya yi daidai da shi. (61) Don irin wannan sakamakon mai girma, ya wajaba masu aiki su yi aiki, saboda wannan shi ne kasuwanci mai riba. (62) Yanzu wannan ni’imar da aka ambata, wadda Allah ya tanadar wa bayinsa waxanda ya tsarkake su don yi masa xa’a, shi ne yafi alheri da xaukaka da matsayi, ko kuwa bishiyar Zaqqum, wadda aka la’anta a cikin Alqur’ani, wadda ita ce abincin kafirai, wanda baya sa qiba, kuma baya wadatar wa daga yunwa?. (63) Haqiqa mun sanya wannan bishiya ta zama fitina ga azzalumai, waxanda suka yi zalunci ta hanyar kafirci da savo, ta inda suka ce: “Tabbas wuta tana cin bishiya, don haka ba zai yiwu a ce bishiya ta tsiro a cikin wuta ba”. (64) Haqiqa bishiyar zaqqum bishiya ce mummuna a tsiron ta, bishiya ce da take tsirowa a tsakiyar wutar Jaheem.**

**(65) ‘Ya’yanta da suke fitowa daga gare ta, basu da kyan gani, tamkar kawunan shaixanu suke. Mummunar kama tana ba da labarin yadda abu yake, don haka wannan yana nufin ‘ya’yanta ba su da daxin xanxano. (66) Haqiqa kafirai zasu ci daga ‘ya’yan ta masu xaci masu muni, su cika cikinsu da babu komai a cikinsa. (67) Sannan bayan sun ci daga wannan bishiya, suna da wani abin sha wanda aka gauraya shi da wani abu, kuma mai muni da zafi. (68) Sannan makomarsu bayan haka tabbas ita ce zuwa wutar jahimu, za su rinqa ciruwa daga azaba zuwa azaba. (69) Waxannan kafirai sun samu iyayensu sun vace daga hanyar shiriya, sai suka yi koyi da su ba tare da wata hujja ba, sai don kwaikwayo kawai. (70) Don haka su, suna bin gurbin iyayensu ne a cikin vata, kuma da gaggawa.**

**(71) Haqiqa da yawa daga cikin mutanen farko sun vace gabaninsu. Don haka, ba mutanenka ba ne – Ya kai wannan Manzo - farkon waxanda suka vace hanya a cikin al’ummu ba. (72) Haqiqa mun aika Manzanni ga waxancan al’ummu na farko, suna tsoratar da su azabar Allah, amma sai suka kafirce. (73) Ka duba - Ya kai wannan Manzo - yaya qarshen mutanen da Manzanninsu suka yi musu gargaxi, amma basu amsa ba ya kasance. Haqiqa qarshen su shiga wuta ne, suna masu dauwama a cikinta, saboda kafircinsu da qaryata Manzanninsu. (74) Sai waxanda Allah ya tsarkake su da yin imani da shi, tabbas za su kuvuta daga azabar da ta zama qarshen waxancan kafirai masu qaryatawa. (75) Haqiqa Annabin mu Nuhu ya kira mu, lokacin da ya yi addu’a ga mutanensa waxanda suka qaryata shi. Madalla da mu masu amsa kiran mai kira, haqiqa mun yi gaggawar amsa mummunar addu’ar da ya yi musu. (76) Haqiqa mun kuvutar da shi da iyalan gidansa, da Muminan da suke tare da shi daga cutarwar mutanensa da kuma nutsewa a ruwan Xufana, wanda aka aikawa kafirai daga cikin mutanensa.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Rabauta da ni’imar Aljannah, shi ne rabo mafi girma, kuma don irin wannan kyauta da falala, ya kamata masu aiki su dage su yi aiki. 2 - Tabbas abincin ‘yan wuta shi ne Zaqqum, ma’abocin ‘ya’yan itatuwa masu xaci, marasa daxi, marasa xanxano, mai wahalar haxiyewa, mai raxaxi wurin ci. 3 - Allah ya amsa addu’ar Annabi Nuhu ta hanyar halakar da mutanensa. Madallah da Allah, wanda ake nufata da buqata, kuma yake amsawa.**

وَجَعَلْنَا ذُرِّيَّتَهُۥ هُمُ ٱلْبَاقِينَ ٧٧ وَتَرَكْنَا عَلَيْهِ فِى ٱلْـَٔاخِرِينَ ٧٨ سَلَٰمٌ
عَلَىٰ نُوحٍ فِى ٱلْعَٰلَمِينَ ٧٩ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجْزِى ٱلْمُحْسِنِينَ ٨٠ إِنَّهُۥ
ثلاثة أرباع الحزب ٤٥ مِنْ عِبَادِنَا ٱلْمُؤْمِنِينَ ٨١ ثُمَّ أَغْرَقْنَا ٱلْـَٔاخَرِينَ ٨٢ ۞ وَإِنَّ مِن
شِيعَتِهِۦ لَإِبْرَٰهِيمَ ٨٣ إِذْ جَآءَ رَبَّهُۥ بِقَلْبٍ سَلِيمٍ ٨٤ إِذْ قَالَ
لِأَبِيهِ وَقَوْمِهِۦ مَاذَا تَعْبُدُونَ ٨٥ أَئِفْكًا ءَالِهَةً دُونَ ٱللَّهِ تُرِيدُونَ
٨٦ فَمَا ظَنُّكُم بِرَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ٨٧ فَنَظَرَ نَظْرَةً فِى ٱلنُّجُومِ ٨٨
فَقَالَ إِنِّى سَقِيمٌ ٨٩ فَتَوَلَّوْا۟ عَنْهُ مُدْبِرِينَ ٩٠ فَرَاغَ إِلَىٰٓ ءَالِهَتِهِمْ
فَقَالَ أَلَا تَأْكُلُونَ ٩١ مَا لَكُمْ لَا تَنطِقُونَ ٩٢ فَرَاغَ عَلَيْهِمْ ضَرْبًۢا
بِٱلْيَمِينِ ٩٣ فَأَقْبَلُوٓا۟ إِلَيْهِ يَزِفُّونَ ٩٤ قَالَ أَتَعْبُدُونَ مَا تَنْحِتُونَ
٩٥ وَٱللَّهُ خَلَقَكُمْ وَمَا تَعْمَلُونَ ٩٦ قَالُوا۟ ٱبْنُوا۟ لَهُۥ بُنْيَٰنًا فَأَلْقُوهُ
فِى ٱلْجَحِيمِ ٩٧ فَأَرَادُوا۟ بِهِۦ كَيْدًا فَجَعَلْنَٰهُمُ ٱلْأَسْفَلِينَ ٩٨
وَقَالَ إِنِّى ذَاهِبٌ إِلَىٰ رَبِّى سَيَهْدِينِ ٩٩ رَبِّ هَبْ لِى مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ
١٠٠ فَبَشَّرْنَٰهُ بِغُلَٰمٍ حَلِيمٍ ١٠١ فَلَمَّا بَلَغَ مَعَهُ ٱلسَّعْىَ قَالَ يَٰبُنَىَّ
إِنِّىٓ أَرَىٰ فِى ٱلْمَنَامِ أَنِّىٓ أَذْبَحُكَ فَٱنظُرْ مَاذَا تَرَىٰ ۚ قَالَ يَٰٓأَبَتِ
ٱفْعَلْ مَا تُؤْمَرُ ۖ سَتَجِدُنِىٓ إِن شَآءَ ٱللَّهُ مِنَ ٱلصَّٰبِرِينَ ١٠٢



**(77) Kuma muka tseratar da iyalansa, da mabiyansa Muminai su kaxai. Haqiqa tabbas mun nutsar da waxanda ba su ba, daga cikin mutanensa kafirai. (78) Muka wanzar masa kyakkyawan ambato a cikin al'ummun da suka zo bayansa, suna ta yabonsa. (79) Kuvuta da aminci sun tabbata ga Annabi Nuhu, babu wani abin kushewa da mutanen baya zasu iya cewa game da shi, kuma haka za'a ci gaba da ambatonsa da alheri. (80) Tabbas irin wannan sakamakon da muka sakawa Annabi Nuhu (A.S) da shi, haka muke sakawa masu kyautata ibadarsu da xa'arsu ga Allah shi kaxai. (81) Tabbas Annabi Nuhu yana cikin bayin mu muminai, masu aiki da xa'ar Allah. (82) Sannan muka nutsar da sauran da ruwan Xufana, wanda muka aiko musu da shi, babu wanda ya rage a cikinsu. (83) Tabbas Annabi Ibrahim yana cikin mabiya addininsa, waxanda suka dace da shi wajen kira zuwa ga kaxaita Allah. (84) Ka ambaci yayin da ya zo wa Ubangijinsa da lafiyayyar zuciya, ga barin shirka, kuma yana mai nasiha ga Allah a cikin halittarsa. (85) Yayin da ya cewa babansa da mutanensa masu yin shirka, yana mai zarginsu: "Me kuke bautawa koma bayan Allah?". (86) "Yanzu allolin qarya kuke bauta wa koma bayan Allah?". (87) Ya ku mutane wane irin zato kuke yi wa Allah Ubangijin talikai, idan kuka haxu da shi alhali kuna bautawa waninsa?. Me kuke ganin zai yi muku?". (88) Sai Annabi Ibrahim ya kalli taurari, yana mai yin tunanin dabarar da zai yi don kada ya fita tare da mutanensa. (89) Sai ya ce yana mai musu bayanin abin da zai hana shi fita tare da mutanensa zuwa ga taron bikinsu: "Tabbas ni, ba ni da lafiya". (90) Sai suka qyale shi suka tafi. (91) Sai ya karkata ya tafi zuwa ga allolinsu waxanda suke bautawa koma bayan Allah, ya ce yana mai izgili ga allolinsu: "Ba kwa cin abincin da mushrikai suke yi muku?". (92) Me ya same ku ba kwa magana, ba kwa amsawa wanda yake roqon ku? Yanzu irin waxannan za a bautawa koma bayan Allah?". (93) Sai Annabi Ibrahim ya nufe su da duka da hannusa na dama, da nufin ya karkarya su. (94) Sai masu bautar gumakan suka nufo shi cikin gaggawa. (95) Sai Annabi Ibrahim ya fuskance su da nutsuwa, ya ce musu, yana mai tsawatar da su: "Yanzu kuna bautawa wasu alloli koma bayan Allah, waxanda ku ne kuke sassaqa su da hannayenku?". (96) Allah mai tsarki shi ne ya halicce ku, ku kanku, kuma ya halicci ayyukan ku, kuma daga cikin ayyukan ku akwai waxannan gumaka, don haka Allah shi ne ya cancanta a bauta masa shi kaxai, kada a shirka da wani tare da shi. (97) Yayin da suka gaza kayar da shi da hujja, sai suka koma amfani da qarfi, sai suka yi shawara a junansu akan me zasu aikatawa Annabi Ibrahim, sai suka ce: "Ku gina wani gini, ku cika shi da qirare, sai ku kunna wuta, sannan sai ku jefa shi a ciki". (98) Mutanen Annabi Ibrahim sun yi mummunan nufi gare shi, na su halaka shi su huta da shi, amma sai muka sa suka zama asararru, yayin da muka sanya wutar ta zama mai sanyi da aminci a gare shi. (99) Sai Annabi Ibrahim ya ce: "Haqiqa ni mai yin hijira ne zuwa ga Ubangijina, zan bar garin mutane na, don in samu damar bautawa Ubangijina, kuma da sannu Ubangijina zai shiryar da ni zuwa ga abin da yake alheri ne a gare ni duniya da lahira. (100) Ya Ubangiji ka azurta ni da xa nagari, wanda zai zama mataimaki a gare ni, kuma makwafin mutane na a cikin wannan baqunci da na shiga. (101) Sai muka amsa masa addu'arsa, muka bashi labarin abin da zai faranta masa rai, inda muka yi masa bushara da xa wanda zai girma, kuma ya zama mai haquri. Wannan xan shi ne Annabi Isma'il (A.S). (102) Yayin da Annabi Isma'il ya zama saurayi, qarfinsa ya kai ya yi irin aikin da babansa yake yi, sai babansa Annabi Ibrahim ya yi mafarki – Mafarkin Annabawa wahayi ne -. Sai Annabi Ibrahim ya ba wa xan sa labarin abin da wannan mafarki ya qunsa ya ce: "Ya kai xana, tabbas ni na gani a barci ina yanka ka, amma ya kake gani za a yi. Sai Annabi Isma'il ya amsawa babansa ya ce: "Ya kai babana, ka aikata abin da Allah ya umarce ka na yanka ni, zaka same ni cikin masu haquri, masu yarda da hukuncin Allah.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Yana daga abin da yake nuna ni'imomin da Allah ya yi wa Annabi Nuhu: kuvutar Annabi Nuhu da waxanda suka yi imani da shi, kuma da sanya zuriyarsa ta zama tushen zuriyar mutane, da jinsi daban daban, da wanzar da ambato mai kyau da yabo a gare shi. 2 - Ayyukan mutun Allah ne yake halittarsu, amma bawa ne yake aikatawa da zavinsa. 3 - Wanda aka so a yanka kamar yadda wannan aya ta nuna, shi ne Annabi Isma'il, saboda shi ne wanda aka fara yi wa babansa bishara da shi tun farko, amma Annabi Ishaq an yi bishara da shi bayan Annabi Isma'il ne. 4 - Faxin Annabi Isma'il: (Zaka same ni in Allah ya yarda cikin masu haquri) shi ne dalilin da ya janyo masa samun dace na haquri, don ya mayar da lamarin ga Allah.**

فَلَمَّآ أَسۡلَمَا وَتَلَّهُۥ لِلۡجَبِينِ ١٠٣ وَنَٰدَيۡنَٰهُ أَن يَٰٓإِبۡرَٰهِيمُ ١٠٤
قَدۡ صَدَّقۡتَ ٱلرُّءۡيَآۚ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١٠٥ إِنَّ
هَٰذَا لَهُوَ ٱلۡبَلَٰٓؤُاْ ٱلۡمُبِينُ ١٠٦ وَفَدَيۡنَٰهُ بِذِبۡحٍ عَظِيمٖ ١٠٧ وَتَرَكۡنَا
عَلَيۡهِ فِي ٱلۡأٓخِرِينَ ١٠٨ سَلَٰمٌ عَلَىٰٓ إِبۡرَٰهِيمَ ١٠٩ كَذَٰلِكَ نَجۡزِي
ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١١٠ إِنَّهُۥ مِنۡ عِبَادِنَا ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١١١ وَبَشَّرۡنَٰهُ
بِإِسۡحَٰقَ نَبِيّٗا مِّنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ١١٢ وَبَٰرَكۡنَا عَلَيۡهِ وَعَلَىٰٓ إِسۡحَٰقَۚ
وَمِن ذُرِّيَّتِهِمَا مُحۡسِنٞ وَظَالِمٞ لِّنَفۡسِهِۦ مُبِينٞ ١١٣ وَلَقَدۡ مَنَنَّا
عَلَىٰ مُوسَىٰ وَهَٰرُونَ ١١٤ وَنَجَّيۡنَٰهُمَا وَقَوۡمَهُمَا مِنَ ٱلۡكَرۡبِ
ٱلۡعَظِيمِ ١١٥ وَنَصَرۡنَٰهُمۡ فَكَانُواْ هُمُ ٱلۡغَٰلِبِينَ ١١٦ وَءَاتَيۡنَٰهُمَا
ٱلۡكِتَٰبَ ٱلۡمُسۡتَبِينَ ١١٧ وَهَدَيۡنَٰهُمَا ٱلصِّرَٰطَ ٱلۡمُسۡتَقِيمَ
١١٨ وَتَرَكۡنَا عَلَيۡهِمَا فِي ٱلۡأٓخِرِينَ ١١٩ سَلَٰمٌ عَلَىٰ مُوسَىٰ
وَهَٰرُونَ ١٢٠ إِنَّا كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١٢١ إِنَّهُمَا
مِنۡ عِبَادِنَا ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١٢٢ وَإِنَّ إِلۡيَاسَ لَمِنَ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ١٢٣
إِذۡ قَالَ لِقَوۡمِهِۦٓ أَلَا تَتَّقُونَ ١٢٤ أَتَدۡعُونَ بَعۡلٗا وَتَذَرُونَ أَحۡسَنَ
ٱلۡخَٰلِقِينَ ١٢٥ ٱللَّهَ رَبَّكُمۡ وَرَبَّ ءَابَآئِكُمُ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٢٦



**(103) Yayin da su biyun suka sunkuya ga Allah, suka miqa wuya gare shi, sai Annabi Ibrahim ya kwantar da xansa a gefen goshinsa, domin ya zartar da umarnin da aka yi masa na yanka shi.**
**(104) Sai muka kirawo Annabi Ibrahim, yana qoqarin zartar da umarnin Allah na yanka xan sa, muka cewa: "Ya Ibrahim". (105) Tabbas ka tabbatar da mafarkin da ka gani a barcinka, ta hanyar azamar ka akan yanka xan ka. Lallai mu kamar yadda muka saka maka, ta hanyar kuvutar da kai daga wannan jarrabawar babba, haka muke sakawa masu kyautatawa, mu kuvutar da su daga jarrabawa da tsanani. (106) Tabbas wannan shi ne jarrabawa bayyananniya, kuma Annabi Ibrahim ya samu nasara a cikinta. (107) Muka fanshi Annabi Isma'il da babban rago, maimakon a yanka shi. (108) Muka wanzar da ambato mai kyau game da Annabi Ibrahim a cikin al'ummun da suka zo daga baya. (109) Gaisuwa daga Allah zuwa gare shi, da addu'ar kuvuta daga duk wata cuta ga Annabi Ibrahim. (110) Kamar yadda muka sakawa Annabi Ibrahim da irin wannan sakamako, saboda xa'arsa, to haka muke sakawa masu kyautatawa. (111) Tabbas Annabi Ibrahim yana cikin bayinmu muminai, waxanda suke cika duk wani abin da bautar Allah ta hukunta, ta yi umarni da shi. (112) Muka yi masa bushara da wani xan, da zai zama Annabi, kuma bawa nagari, shi ne Ishaq, sakamakon xa'arsa cikin yanka xan sa xaya tal, shi ne Isma'il. (113) Kuma muka saukar masa da albarka daga wajen mu, shi da xan sa Ishaq, muka yawaita musu ni'ima, daga ciki akwai yawaita musu 'ya'yansu. Daga cikin zuriyar su akwai mai kyautata xa'a ga Ubangijinsa, a cikin su akwai mai zaluntar kansa, zalunci na fili, da yin kafirci da aikata savon Allah. (114) Haqiqa mun yi baiwar Annabta ga Annabi Musa da xan uwansa Annabi Haruna. (115) Muka kuvutar da su da mutanen su – bani Israila - daga bautarwar da Fir'auna yake yi musu, kuma daga nutsewa a teku. (116) Kuma muka taimake su a kan Fir'auna da sojojinsa, don haka rinjaye ya zama nasu ne a kan abokan gabarsu. (117) Kuma mun ba wa Annabi Musa da xan-uwansa Annabi Haruna littafin Attaura, littafi daga wajen Allah, bayyananne wanda babu wani duhu a cikinsa. (118) Muka shiryar da su ga tafarki madaidaici, wanda babu karkata a cikinsa, shi ne tafarkin addinin musulunci, wanda yake sadarwa zuwa ga yardar Allah Mahalicci mai tsarki. (119) Kuma muka wanzar musu da kyakkyawan ambato a cikin al'ummun da suka zo a bayansu. (120) Gaisuwa daga Allah mai daxi gare su, da yabo da addu'ar kuvuta daga duk wani abin qi gare su. (121) Haqiqa mu kamar yadda muka sakawa Annabi Musa da Annabi Haruna wannan sakamako mai kyau, haka muke sakawa masu kyautatawa, saboda xa'arsu ga Ubangijin su. (122) Tabbas Annabi Musa da Annabi Haruna suna cikin bayin mu, masu imani da Allah, da aiki da abin da ya shar'anta. (123) Tabbas Annabi Ilyasu yana cikin Manzanni daga Ubangijinsa, Allah ya yi masa baiwa da Annabta da Manzanci.**
**(124) A yayin da ya cewa mutanensa cikin bani Isra'ila: "Ya ku mutane na, yanzu baza ku ji tsoron Allah ba? Ta hanyar kamanta umarninsa, wanda daga cikin su akwai kaxaita Allah. Da kuma nisantar abubuwan da ya hana, wanda daga cikinsu akwai shirka. (125) Yanzu kwa riqa bautawa gunkin ku (Ba'alu) ku bar bautawa Allah, wanda shi ne mafi kyautatawar masu halitta?. (126) Kuma Allah shi ne Ubangijinku, wanda ya halicce ku, kuma ya halicci iyayen ku gabanin ku, shi ne ya cancanta a bauta masa, ba wasu gumaka ba , waxanda ba sa amfanarwa ko cutarwa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Faxin Allah: (Yayin da suka miqa wuya) dalili ne akan cewa Annabi Ibrahim da Annabi Isma'il sun kai matuqa wajen miqa wuya ga umarnin Allah. 2 - Yana daga manufofin shari'a yantar da bayi daga bautar mutane.**
**3 - Kyakkyawan ambato yana daga cikin ni'imar da Allah yake gaggauto da ita a duniya.**

فَكَذَّبُوهُ فَإِنَّهُمْ لَمُحْضَرُونَ ١٢٧ إِلَّا عِبَادَ ٱللَّهِ ٱلْمُخْلَصِينَ ١٢٨
وَتَرَكْنَا عَلَيْهِ فِي ٱلْآخِرِينَ ١٢٩ سَلَٰمٌ عَلَىٰٓ إِلْ يَاسِينَ ١٣٠ إِنَّا
كَذَٰلِكَ نَجْزِي ٱلْمُحْسِنِينَ ١٣١ إِنَّهُۥ مِنْ عِبَادِنَا ٱلْمُؤْمِنِينَ
١٣٢ وَإِنَّ لُوطًا لَّمِنَ ٱلْمُرْسَلِينَ ١٣٣ إِذْ نَجَّيْنَٰهُ وَأَهْلَهُۥٓ أَجْمَعِينَ
١٣٤ إِلَّا عَجُوزًا فِي ٱلْغَٰبِرِينَ ١٣٥ ثُمَّ دَمَّرْنَا ٱلْآخَرِينَ ١٣٦ وَإِنَّكُمْ
لَتَمُرُّونَ عَلَيْهِم مُّصْبِحِينَ ١٣٧ وَبِٱلَّيْلِ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ١٣٨ وَإِنَّ
يُونُسَ لَمِنَ ٱلْمُرْسَلِينَ ١٣٩ إِذْ أَبَقَ إِلَى ٱلْفُلْكِ ٱلْمَشْحُونِ ١٤٠
فَسَاهَمَ فَكَانَ مِنَ ٱلْمُدْحَضِينَ ١٤١ فَٱلْتَقَمَهُ ٱلْحُوتُ وَهُوَ مُلِيمٌ
١٤٢ فَلَوْلَآ أَنَّهُۥ كَانَ مِنَ ٱلْمُسَبِّحِينَ ١٤٣ لَلَبِثَ فِي بَطْنِهِۦٓ إِلَىٰ يَوْمِ
يُبْعَثُونَ ١٤٤ ۞ فَنَبَذْنَٰهُ بِٱلْعَرَآءِ وَهُوَ سَقِيمٌ ١٤٥ وَأَنۢبَتْنَا الحزب ٤٦
عَلَيْهِ شَجَرَةً مِّن يَقْطِينٍ ١٤٦ وَأَرْسَلْنَٰهُ إِلَىٰ مِاْئَةِ أَلْفٍ أَوْ
يَزِيدُونَ ١٤٧ فَـَٔامَنُوا۟ فَمَتَّعْنَٰهُمْ إِلَىٰ حِينٍ ١٤٨ فَٱسْتَفْتِهِمْ
أَلِرَبِّكَ ٱلْبَنَاتُ وَلَهُمُ ٱلْبَنُونَ ١٤٩ أَمْ خَلَقْنَا ٱلْمَلَٰٓئِكَةَ إِنَٰثًا
وَهُمْ شَٰهِدُونَ ١٥٠ أَلَآ إِنَّهُم مِّنْ إِفْكِهِمْ لَيَقُولُونَ ١٥١ وَلَدَ
ٱللَّهُ وَإِنَّهُمْ لَكَٰذِبُونَ ١٥٢ أَصْطَفَى ٱلْبَنَاتِ عَلَى ٱلْبَنِينَ ١٥٣



**(127) Babu abin da mutanen sa suka yi face sun qaryata shi, kuma saboda qaryatawar su tabbas za a halarto da su cikin azaba. (128) Sai dai wanda ya kasance mumini ne daga cikin mutanen sa, mai tsarkake Allah a cikin bautar sa, to wannan tabbas zai kuvuta daga halartowa cikin azaba.**
**(129) Muka wanzar masa da yabo da ambato mai kyau a cikin al'ummun da suka zo bayansa.**
**(130) Gaisuwa daga Allah da yabo ga Annabi Ilyasu.**
**(131) Tabbas mu kamar yadda muka sakawa Annabi Ilyasu irin wannan sakamako, to haka muke sakawa masu kyautatawa a cikin bayin mu muminai. (132) Tabbas Annabi Ilyasu yana cikin bayin mu muminai na haqiqa, masu gaskiya cikin imaninsu da Ubangijinsu. (133) Tabbas Annabi Luxu yana cikin Manzannin Allah, waxanda ya aiko su zuwa ga mutanensu, su yi bushara da gargaxi. (134) Ka ambaci lokacin da muka kuvutar da shi da iyalansa daga azabar da muka aiko wa mutanensa. (135) Sai dai matarsa, mace ce wadda azabar mutanen ta ta haxa da ita, saboda kasancewar ta kafira kamar su. (136) Sannan muka halakar da sauran mutanensa, masu qaryatawa, kuma basu gasgata abin da yazo da shi ba.**
**(137) Tabbas ku - Mutanen Makkah - kuna wucewa ta gidajensu a tafiye – tafiyenku zuwa Sham da safe. (138) Haka ma kuna wuce su da daddare, ba zaku hankalta ba? ku wa'azantu da yadda lamarinsu ya qare bayan qaryatawar su, da kafircewar su, da aikata alfashar da ba wanda ya riga su?. (139) Tabbas bawan mu Annabi Yunus yana cikin Manzannin Allah, waxanda Allah ya aiko su zuwa ga mutanensu, suna musu bushara, kuma suna musu gargaxi. (140) Yayin da ya gujewa mutanensa ba tare da izinin Ubangijinsa ba, ya hau jirgin ruwa da yake cike da mutane da kayansu. (141) Sai jirgin ruwan ya kusa nutsewa, saboda cikar da ya yi, sai mutanen da suke ciki suka yi quri'a, don su jefa wasu daga cikinsu, don gudun nutsewar jirgin ruwan, saboda yawan mutanen da suke ciki. Sai Annabi Yunus ya zama cikin waxanda aka yi galaba a kansu, don haka sai suka jefa shi cikin teku. (142) Yayin da suka jefa shi sai kifi ya kama shi, ya haxiye shi, yana mai aikata abin da aka zarge shi a kai, saboda ya tafi zuwa teku ba tare da an ba shi izini ba. (143) Ba don Annabi Yunus ya kasance daga cikin masu ambaton Allah da yawa ba, tun kafin wannan abin ya same shi, ba don tasbihin yake yi a cikin kifin ba. (144) Tabbas da ya zauna a cikin cikin kifin har zuwa ranar alqiyama, ta yadda zai zamar masa qabari. (145) Sai muka jefo shi daga cikin kifin, a wani wuri da babu komai na bishiya ko gini, yana mai raunin jiki, saboda ya shafe wani lokaci a cikin kifi. (146) Kuma muka tsirar masa da wata itaciya - mai kamar kabewa - a wannan qasar da ba komai, don ya riqa yin inuwa da ita, yana ci daga gare ta. (147) Sai muka aika shi zuwa ga mutanensa, da yawansu ya kai dubu xari, koma sun fi haka. (148) Sai suka yi imani, suka gasgata abin da ya zo da shi, sai Allah ya jiyar da su daxi a rayuwarsu ta duniya har zuwa lokacin da ajalinsu da aka qayyade musu ya cika. (149) Ya Muhammad ka tambayi mushirikai, tambaya ta inkari ka ce: "Yanzu kuna sa wa Allah 'ya'ya mata, waxanda kuke qin su, ku sa wa kanku 'yaya maza, waxanda kuke so, wannan wane irin rabo ne".**
**(150) Ta yaya suke riya cewa Mala'iku mata ne, alhali ba sa nan lokacin da aka halicce su, kuma basu gani ba?"**
**(151) Ku saurara! Lallai mushirikai saboda qaryarsu da qiren su ga Allah. (152) Suna rava masa xa, sai tabbas qarya suke a cikin wannan da'awar ta su. (153) Shin Allah ya zavar wa kansa 'ya'ya mata, waxanda kuke qi a kan 'ya'ya maza, waxanda kuke so? Sam ba haka ba ne.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Yana daga tsarin Allah, wanda baya canzawa: kuvutar da muminai, da halakar da kafirai. 2 - Wajibcin wa'azantuwa da xaukan izina da makomar waxanda suka qaryata Manzanni, don kada abin da ya same su, ya samu wanin su. 3 - Halaccin yin amfani da quri'a, saboda faxin Allah maxaukakin sarki: "Sai ya kaxa quri'arsa, sai ya kasance daga cikin waxanda aka rinjaya".**

مَا لَكُمْ كَيْفَ تَحْكُمُونَ ١٥٤ أَفَلَا تَذَكَّرُونَ ١٥٥ أَمْ لَكُمْ سُلْطَانٌ مُّبِينٌ ١٥٦
فَأْتُوا بِكِتَابِكُمْ إِن كُنتُمْ صَادِقِينَ ١٥٧ وَجَعَلُوا بَيْنَهُ وَبَيْنَ الْجِنَّةِ
نَسَبًا ۚ وَلَقَدْ عَلِمَتِ الْجِنَّةُ إِنَّهُمْ لَمُحْضَرُونَ ١٥٨ سُبْحَانَ اللَّهِ عَمَّا
يَصِفُونَ ١٥٩ إِلَّا عِبَادَ اللَّهِ الْمُخْلَصِينَ ١٦٠ فَإِنَّكُمْ وَمَا تَعْبُدُونَ ١٦١
مَا أَنتُمْ عَلَيْهِ بِفَاتِنِينَ ١٦٢ إِلَّا مَنْ هُوَ صَالِ الْجَحِيمِ ١٦٣ وَمَا مِنَّا إِلَّا
لَهُ مَقَامٌ مَّعْلُومٌ ١٦٤ وَإِنَّا لَنَحْنُ الصَّافُّونَ ١٦٥ وَإِنَّا لَنَحْنُ الْمُسَبِّحُونَ
١٦٦ وَإِن كَانُوا لَيَقُولُونَ ١٦٧ لَوْ أَنَّ عِندَنَا ذِكْرًا مِّنَ الْأَوَّلِينَ ١٦٨ لَكُنَّا
عِبَادَ اللَّهِ الْمُخْلَصِينَ ١٦٩ فَكَفَرُوا بِهِ ۖ فَسَوْفَ يَعْلَمُونَ ١٧٠ وَلَقَدْ
سَبَقَتْ كَلِمَتُنَا لِعِبَادِنَا الْمُرْسَلِينَ ١٧١ إِنَّهُمْ لَهُمُ الْمَنصُورُونَ ١٧٢
وَإِنَّ جُندَنَا لَهُمُ الْغَالِبُونَ ١٧٣ فَتَوَلَّ عَنْهُمْ حَتَّىٰ حِينٍ ١٧٤ وَأَبْصِرْهُمْ
فَسَوْفَ يُبْصِرُونَ ١٧٥ أَفَبِعَذَابِنَا يَسْتَعْجِلُونَ ١٧٦ فَإِذَا نَزَلَ بِسَاحَتِهِمْ
فَسَاءَ صَبَاحُ الْمُنذَرِينَ ١٧٧ وَتَوَلَّ عَنْهُمْ حَتَّىٰ حِينٍ ١٧٨ وَأَبْصِرْ
فَسَوْفَ يُبْصِرُونَ ١٧٩ سُبْحَانَ رَبِّكَ رَبِّ الْعِزَّةِ عَمَّا يَصِفُونَ
١٨٠ وَسَلَامٌ عَلَى الْمُرْسَلِينَ ١٨١ وَالْحَمْدُ لِلَّهِ رَبِّ الْعَالَمِينَ ١٨٢

آيَاتُهَا ٨٨ سُورَةُ صٓ تَرْتِيبُهَا ٣٨



**(154) Me ya same ku ne - Ya ku mushrikai - kuke yin irin wannan ja'irin hukunci, kuke sanyawa Allah 'ya'ya mata, ku kuma ku sanyawa kanku 'ya'ya maza?. (155) Shin ba zaku iya tuna vacin abin da kuke kai ba, na wannan mummunar aqidar? Domin Haqiqa da kuna yin tunani da baku faxi wannan maganar ba. (156) Ko kuwa kuna da wata hujja bayyananniya, ko wani dalili a fili, daga wani littafi ko wani Manzo da ya zo da hakan?.**
**(157) To ku zo da littafin da yake xauke da hujja a kan haka, idan har da gaske kuke a cikin da'awar da kuke yi. (158) Mushirikai sun sanya dangantaka (Nasaba) tsakanin Mala'iku, waxanda basa ganin su da Allah, a yayin da suka riya cewa, Mala'iku 'ya'yan Allah ne mata. Amma tabbas Mala'iku sun san Allah zai halarto da mushirikai don a yi musu hisabi. (159) Allah ya tsarkaka kuma ya girmama daga abin da mushirikai suke siffata shi da shi, na daga abin da bai dace da shi ba, na xa da abokin tarayya da makamantan su. (160) Sai dai bayin Allah, da Allah ya tsarkake su, haqiqa su basa siffata Allah sai da abin da ya dace da shi na siffofin girma da cika. (161) Lallai ku – Mushirikai - da abin da kuke batawa ba Allah ba. (162) Baku isa ku vatar da wani daga addinin gaskiya ba.**
**(163) Sai dai wanda Allah ya hukunta cewa shi xan wuta ne, to sai Allah ya zartar da abin da ya hukunta a kansa, sai ya kafirta, ya shiga wuta. Amma ku da ababen bautar baku da iko a kan haka. (164) Mala'iku suka ce - suna masu bayyana bautarsu ga Allah, da barrantar su daga abin da mushrikai suke riyawa: "Babu wani daga cikin mu face yana da matsayi sananne, a cikin bautar Allah da yi masa xa'a". (165) (166) Kuma tabbas mu Mala'iku muna tsayawa ne a cikin sahu sahu wurin bautar Allah da yi masa xa'a. kuma mu masu tsarkake Allah ne daga duk abin da bai dace da shi ba na siffofi. (167) (168) (169) (170) Haqiqa Mushirikai cikin mutanen Makkah, sun kasance suna cewa gabanin aiko Annabi Muhammad (S.AW): "Da muna da wani littafi, daga cikin littattafan mutanen farko, kamr Attaura, da mun tsarkake bauta ga Allah, alhalin qarya suke yi. Saboda Annabi Muhammad ya zo musu da Alqur'ani, amma sai suka kafirce da shi. Da sannu zasu san abin da yake jiran su na azaba mai raxaxi ranar alqiyama. (171) (172) (173) Haqiqa kalmar mu da babu wanda ya isa ya canzata, ta rigaya cewa, babu mai mayar da Manzannin mu, kuma su ne waxanda za su yi nasara a kan abokan gabarsu, saboda abin da Allah ya yi musu baiwa da shi na hujja da qarfi, kuma tabbas rinjaye yana ga rundunar mu, waxanda suke yin yaqi saboda Allah, don kalmar Allah ta zama ita ce maxaukakiya. (174) Ya kai wannan Manzo, ka kawar da kai ga barin waxannan mushirikai, masu taurin kai har zuwa wani lokaci da Allah ne ya sani, har lokacin azabar su ya zo.**
**(175) Ka saurara musu har lokacin da azaba zata sauka a kansu, a lokacin ne za su gani, kuma ganin ba zai yi musu amfani ba. (176) Yanzu waxannan mushirikai suna gaggawar azabar Allah ta zo musu ne?.**
**(177) To idan har azabar Allah ta saukar musu, to tir da wannan safiyar ta su. (178) Ya kai wannan Manzo, ka kawar da kai daga barinsu, har Allah ya yanke musu hukunci na yi musu azaba. (179) Kuma ka jira, su ma waxannan za su jira abin da zai same su na azabar Allah da uqubarsa. (180) Ubangijinka - Ya Muhammad - ya tsarkaka, Ubangiji mai qarfi, kuma ya tsarkaka daga duk abin da mushrikai suke siffata shi, na siffofin tawaya.**
**(181) Gaisuwar Allah da yabonsa sun tabbata ga Manzanninsa masu girma. (182) Kuma dukkan yabo ya tabbata ga Allah, shi ne ya cancance shi, kuma shi ne Ubangijin talikai baki xaya, basu da wani Ubangiji wanda ba shi ba.**
**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Tsarin Allah shi ne taimakon Manzanni da magadansu, ta hanyar hujja da samun rinjaye, kuma a cikin ayoyin akwai bushara mai girma ga wanda ya siffatu da zama cikin rundunar Allah, lallai zai samu galaba da nasara. 2 - A cikin ayoyin a kwai hujja dake tabbatar da gazawar mushrikai, da gazawar allolinsu, game da iya vatar da wani daga cikin bayi, kuma bushara ce ga bayin Allah masu tsarkake zukatansu, cewa Allah zai kuvutar da su daga vatarwar vatattu masu vatarwa.**

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

صٓۚ وَٱلْقُرْءَانِ ذِى ٱلذِّكْرِ ١ بَلِ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ فِى عِزَّةٍ وَشِقَاقٍ ٢
كَمْ أَهْلَكْنَا مِن قَبْلِهِم مِّن قَرْنٍ فَنَادَوا۟ وَّلَاتَ حِينَ مَنَاصٍ ٣ وَعَجِبُوٓا۟
أَن جَآءَهُم مُّنذِرٌ مِّنْهُمْ ۖ وَقَالَ ٱلْكَٰفِرُونَ هَٰذَا سَٰحِرٌ كَذَّابٌ ٤
أَجَعَلَ ٱلْءَالِهَةَ إِلَٰهًا وَٰحِدًا ۖ إِنَّ هَٰذَا لَشَىْءٌ عُجَابٌ ٥ وَٱنطَلَقَ ٱلْمَلَأُ
مِنْهُمْ أَنِ ٱمْشُوا۟ وَٱصْبِرُوا۟ عَلَىٰٓ ءَالِهَتِكُمْ ۖ إِنَّ هَٰذَا لَشَىْءٌ يُرَادُ ٦
مَا سَمِعْنَا بِهَٰذَا فِى ٱلْمِلَّةِ ٱلْءَاخِرَةِ إِنْ هَٰذَآ إِلَّا ٱخْتِلَٰقٌ ٧ أَءُنزِلَ
عَلَيْهِ ٱلذِّكْرُ مِنۢ بَيْنِنَا ۚ بَلْ هُمْ فِى شَكٍّ مِّن ذِكْرِى ۖ بَل لَّمَّا يَذُوقُوا۟ عَذَابِ
٨ أَمْ عِندَهُمْ خَزَآئِنُ رَحْمَةِ رَبِّكَ ٱلْعَزِيزِ ٱلْوَهَّابِ ٩ أَمْ لَهُم مُّلْكُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا ۖ فَلْيَرْتَقُوا۟ فِى ٱلْأَسْبَٰبِ ١٠ جُندٌ
مَّا هُنَالِكَ مَهْزُومٌ مِّنَ ٱلْأَحْزَابِ ١١ كَذَّبَتْ قَبْلَهُمْ قَوْمُ نُوحٍ
وَعَادٌ وَفِرْعَوْنُ ذُو ٱلْأَوْتَادِ ١٢ وَثَمُودُ وَقَوْمُ لُوطٍ وَأَصْحَٰبُ
لْـَٔيْكَةِ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلْأَحْزَابُ ١٣ إِن كُلٌّ إِلَّا كَذَّبَ ٱلرُّسُلَ
فَحَقَّ عِقَابِ ١٤ وَمَا يَنظُرُ هَٰٓؤُلَآءِ إِلَّا صَيْحَةً وَٰحِدَةً مَّا لَهَا
مِن فَوَاقٍ ١٥ وَقَالُوا۟ رَبَّنَا عَجِّل لَّنَا قِطَّنَا قَبْلَ يَوْمِ ٱلْحِسَابِ ١٦



# Suratu Saad

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Ambaton jayayya da varna, da bayanin qarshen mai yin haka.**

**Tafsir:** **(1) (Saad). Bayanin ire iren waxannan haruffa ya gabata a farkon suratul Baqara. Ina rantsuwa da Alqur'ani, wanda ya qunshi wa'azantar da mutane da abin da zai amfane su a duniyar su da lahirar su. Lamarin ba kamar yadda mushrikai suke zato ba ne, na samuwar wasu abokan tarayya tare da Allah. (2) Sai dai kafirai suna cikin qabilanci da girman kai ga barin kaxaita Allah, da savani da Annabi Muhammad (S.A.W), da adawa da shi. (3) Da yawa mun halakar da qarnukan da suka qaryata Manzanninsu, sai suka riqa kira suna masu neman taimako a lokacin da azaba ta saukar musu, amma lokacin ba na kuvuta ba ne daga azaba, ballantana neman taimako ya yi musu amfani. (4) Sun yin mamaki lokacin da Manzo ya zo musu daga cikinsu, yana tsoratar da su azabar Allah, idan har suka ci gaba da yin kafircinsu. Kafirai suka ce yayin da suka ga dalilai masu tabbatar da gaskiyar abin da Annabi Muhammad (S.A.W) ya zo da shi, suka ce: "Wannan mutumin matsafi ne, yana yi wa mutane tsafi, kuma maqaryaci ne cikin da'awar da yake yi cewa shi Manzo ne daga Allah, da ake yi masa wahayi. (5) Yanzu wannan mutumin ya mayar da alloli da yawa sun koma abin bauta guda xaya tal, babu wani abin bauta wanda ba shi ba? Lallai wannan abin da ya yi ya kai matuqa wurin ban mamaki. (6) Sai shugabannin su da manyansu suka tafi suna cewa mabiyansu: "Ku ci gaba da abin da kuke a kai, kada ku shiga addinin Muhammad, ku tabbata a kan bautar allolin ku, abin da Muhammad yake kiran ku na bautawa Allah shi kaxai, wani abu ne shiryayye, kawai yana so ya samu xaukaka a kanmu ne, mu zama mabiyansa". (7) Ba mu tava jin irin abin da Muhammad yake kiran mu zuwa gare shi ba na kaxaita Allah, a cikin abin da muka samu iyayen mu a kansa, koda a cikin addinin Annabi Isa (A.S). Kai! Wannan abin da muka ji ba komai ba ne face qarya da qire". (8) Yanzu zai yi wu a ce shi kaxai a cikinmu aka saukarwa da Alqur'ani, yake kevanta da shi, ba za a saukar mana ba alhali mu ne shugabanni manya?. Kawai dai waxannan mushirikai suna cikin shakku ne game da abin da ake saukar maka na wahayi, kuma basu xanxani azabar Allah ba ne, don haka sai suka ruxu da jinkirin da ake yi musu, da sun xanxani azaba da ba su yi gangancin yin kafirci da shirka da Allah ba, da kuma yin shakku cikin abin da aka saukar maka. (9) Ko kuwa waxannan mushirikai masu qaryatawa suna da taskar falalar Ubangijinka ne, Mabuwayi wanda babu wanda yake rinjayarsa, wanda yake ba da abin da ya ga dama ga wanda ya ga dama, daga cikin taskar falalarsa akwai Annabta, sai ya bada ita ga wanda ya ga dama, don haka Annabta ba ta su ba ce, ballantana su ba wa wanda suka ga dama, ko su hana wanda suka ga dama. (10) Ko kuwa suna da mulkin sammai da mulkin qassai, da abin da yake tsakanin su? don haka suka cancanci su bayar ko su hana? Idan har haka suke riyawa, to su yi riqo da hanyoyin da zasu kai su ga sama mana, don su samu damar yanke hukuncin abin da suka ga dama, na bayarwa ko hanawa? Amma fa ba zasu tava iya hakan ba. (11) Waxannan masu qaryata Annabi Muhammad (S.A.W) runduna ce marar nasara, kamar waxanda suka gabace su daga rundunoni, waxanda suka qaryata Manzanninsu. (12) Waxannan da suka qaryata ba su ne farkon waxanda suka qaryata Manzanni ba, mutanen Annabi Nuhu sun qaryata, haka ma adawa sun qaryata, haka ma Fir'auna ma ma'abocin turaku da yake azabtar da mutane da su ya qaryata. (13) Samudawa ma sun qaryata, mutanen Annabi Luxu ma sun qaryata, mutanen Annabi shu'aibu ma sun qaryata, waxannan su ne waxanda suka yi cincirindon qaryata Manzanni, da kafircewa abin da suka zo da shi. (14) Babu wani daga cikin waxannan cincirindon da bai qaryata Manzo ba, don haka sai azabar Allah ta sauka a kansu, ko da kuwa azabar ta yi jinkiri zuwa wani lokaci. (15) Waxannan masu qaryata Annabi Muhammad (S.A.W) ba komai suke jira ba face a yi busa ta biyu a cikin qaho, wadda babu kome zuwa duniya daga ita, sai azaba ta afka musu matukar suka mutu a kan qaryatawar su. (16) Suka ce cikin izgili: "Ya Ubangijinmu, ka gaggauta turo mana da rabonmu na azaba tun a duniya, kafin ma tashin alqiyama.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Allah ya rantse da Alqur'ani mai girma, don haka ya wajaba a karve shi da imani da gasgatawa, a fuskance shi don fito da ma'anoninsa 2 - Ma'auni na abin duniya shi ya rinjayi mushirikai, har suke tunanin a saukar da Alqur'ani ga manya manyan quraishawa. 3 - Dalilin bada bayan da kafirai suka yiwa imani shi ne: girman kai, fankama, qasaita ga barin bin gaskiya.**

(17) Ka yi haquri - Ya kai wannan Manzo – a kan abin da waxannan masu qaryatawa suke fada, daga abin da baka yarda da shi ba. Kuma ka ambaci bawan mu Annabi Dawud, ma'abocin karfi wurin rinjayar abokan gabarsa, da haquri a kan yi wa Allah xa'a, kuma lallai shi mai yawan komawa ne ga Allah da tuba, da aiki da abin da zai yardar da Allah. (18) Haqiqa mun hore duwatsu tare da Annabi Dawud, suna yin tasbihi yayin da ya yi tasbihi a qarshen yini da farkonsa, yayin vullowar rana. (19) Kuma muka hore masa tsuntsaye da suke iya tsayawa a sama, duk wani mai biyayya yana yin tasbihi bayan Annabi Dawud ya yi. (20) Kuma muka qarfafi mulkinsa da abubuwan da muka ba shi na kwarjini, da karfi, da samun nasara a kan abokan gabarsa, kuma muka ba shi Annabta, da dacewa da daidai a cikin al'amuransa. Muka ba shi iya bayani mai gamsarwa, da rarrabewa a cikin magana da hukunci. (21) Ya kai wannan Manzo, shin labarin masu jayayya ya zo maka, yayin da suka haurowa Annabi Dawud wurin da yake ibadarsa. (22) A yayin da suka shigo wa Annabi Dawud batare da tsammani ba, sai ya razana saboda yadda suka shigo masa ba tsammani, ta wata hanyar da ba a saba da ita ba, da suka fahimci ya firgita sai suka ce masa: "Kada ka ji tsoro, mu masu rigima ne da juna, xayan mu ya cuci xaya, don haka ka yi hukunci a tsakaninmu da adalci, kada ka yi zalunci a tsakanin mu idan kana mana hukunci, kuma ka shiryar da mu zuwa ga tafarkin da yake shi ne tafarki madaidaici. (23) Sai xaya daga cikin masu husumar ya cewa Annabi Dawud: "Wannan mutumin xan uwana ne, yana da tumaki guda casa'in da tara, ni kuma ina da tunkiya guda xaya, sai ya nemi in ba shi ita, kuma ya rinjaye ni da hujja". (24) Sai Annabi Dawud ya yi hukunci a tsakaninsu, ya cewa mai qara: "Tabbas xan uwanka ya zalunce ka da ya roqe ka haxa masa tunkiyar ka zuwa ga tumakinsa, kuma da yawa daga cikin abokan tarayya, sashen su yana cutar da sashe, ta hanyar karvar haqqoqinsa da rashin yi masa adalci, sai muminai, waxanda suke aikata ayyuka nagari, to waxannan su ne kawai suke yi wa abokan hulxar su adalci, basa zaluntar su, sai dai waxanda suka siffatu da haka 'yan kaxan ne. Daga nan sai Annabi Dawud ya tabbatar mun afkar da shi cikin jarrabawa ne da wannan husuma, sai ya nemi gafara daga Ubangijinsa, don neman kusanci ga Allah, kuma ya faxi yayi sujjada, domin samun kusanci gareshi, ya tuba zuwa gare shi. Wannan misali ne Allah ya buga shi game da abin da ya faru da Annabi Dawud na fitina a cikin harkar mace. (25) Sai muka karva masa, muka gafarta masa wannan, lallai shi a wurinmu yana cikin makusanta, kuma yana da kyakkyawar makoma a lahira. (26) Ya kai Dawud haqiqa mun sanya ka halifa a bayan qasa, kana zartar da hukunce-hukunce da al'amuran addini da na duniya, don haka ka yi hukunci a tsakanin mutane bisa adalci, kada ka biyewa son rai a cikin hukuncin ka a tsakanin mutane, kamar ka karkata ga wani daga cikin abokan husuma, saboda kusacinsa da kai, ko abota, ko kuma ka bashi baya saboda kana gaba da shi, sai son rai ya vatar da kai daga tafarki madaidaici, tabbas waxanda suke vacewa daga tafarkin Allah madaidaici suna da azaba mai qarfi, saboda sun manta da ranar hisabi, domin da suna tune da ita, suna tsoronta, da basu biyewa son zukatan su ba.

ٱصۡبِرۡ عَلَىٰ مَا يَقُولُونَ وَٱذۡكُرۡ عَبۡدَنَا دَاوُۥدَ ذَا ٱلۡأَيۡدِۖ إِنَّهُۥٓ أَوَّابٌ ١٧ إِنَّا
سَخَّرۡنَا ٱلۡجِبَالَ مَعَهُۥ يُسَبِّحۡنَ بِٱلۡعَشِيِّ وَٱلۡإِشۡرَاقِ ١٨ وَٱلطَّيۡرَ
مَحۡشُورَةٗۖ كُلّٞ لَّهُۥٓ أَوَّابٞ ١٩ وَشَدَدۡنَا مُلۡكَهُۥ وَءَاتَيۡنَٰهُ ٱلۡحِكۡمَةَ
الحزب ٤٦ وَفَصۡلَ ٱلۡخِطَابِ ٢٠ ۞ وَهَلۡ أَتَىٰكَ نَبَؤُاْ ٱلۡخَصۡمِ إِذۡ تَسَوَّرُواْ
ٱلۡمِحۡرَابَ ٢١ إِذۡ دَخَلُواْ عَلَىٰ دَاوُۥدَ فَفَزِعَ مِنۡهُمۡۖ قَالُواْ لَا تَخَفۡۖ
خَصۡمَانِ بَغَىٰ بَعۡضُنَا عَلَىٰ بَعۡضٖ فَٱحۡكُم بَيۡنَنَا بِٱلۡحَقِّ وَلَا تُشۡطِطۡ
وَٱهۡدِنَآ إِلَىٰ سَوَآءِ ٱلصِّرَٰطِ ٢٢ إِنَّ هَٰذَآ أَخِي لَهُۥ تِسۡعٞ وَتِسۡعُونَ نَعۡجَةٗ
وَلِيَ نَعۡجَةٞ وَٰحِدَةٞ فَقَالَ أَكۡفِلۡنِيهَا وَعَزَّنِي فِي ٱلۡخِطَابِ ٢٣ قَالَ
لَقَدۡ ظَلَمَكَ بِسُؤَالِ نَعۡجَتِكَ إِلَىٰ نِعَاجِهِۦۖ وَإِنَّ كَثِيرٗا مِّنَ ٱلۡخُلَطَآءِ لَيَبۡغِي
بَعۡضُهُمۡ عَلَىٰ بَعۡضٍ إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَقَلِيلٞ
سجدة مَّا هُمۡۗ وَظَنَّ دَاوُۥدُ أَنَّمَا فَتَنَّٰهُ فَٱسۡتَغۡفَرَ رَبَّهُۥ وَخَرَّۤ رَاكِعٗاۤ وَأَنَابَ ۩
٢٤ فَغَفَرۡنَا لَهُۥ ذَٰلِكَۖ وَإِنَّ لَهُۥ عِندَنَا لَزُلۡفَىٰ وَحُسۡنَ مَـَٔابٖ ٢٥
يَٰدَاوُۥدُ إِنَّا جَعَلۡنَٰكَ خَلِيفَةٗ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَٱحۡكُم بَيۡنَ ٱلنَّاسِ بِٱلۡحَقِّ
وَلَا تَتَّبِعِ ٱلۡهَوَىٰ فَيُضِلَّكَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَضِلُّونَ
عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ لَهُمۡ عَذَابٞ شَدِيدُۢ بِمَا نَسُواْ يَوۡمَ ٱلۡحِسَابِ ٢٦



**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** 1 - Bayanin falalar Annabin Allah Dawud, da abin da Allah ya kevance shi da su na ayoyi. 2 - Annabawa tsira da amincin Allah su tabbata a gare su, ababen karewa ne daga yin kuskure a cikin abin da suke isar wa na saqon Allah, saboda manufar saqon baza ta tabbata ba sai da hakan, sai dai wasu abubuwa na xabi'a, kamar mantuwa, ko rafkana ga wani hukunci, suna iya faruwa gare su, sai dai shi ma Allah yana riskar su da rangwamen sa da tausayinsa. 3 - Wasu cikin malamai sun kafa hujja da faxin Allah da yake cewa: (kuma da yawa daga cikin abokan hulxa, sashensu yana zaluntar sashi) akan halaccin haxin gwiwa tsakanin mutum biyu ko fiye da haka a kan wani lamari. 4 - Ya kamata a lazimci ladabi da nutsuwa yayin da za a shiga wurin ma'abota falala da matsayi.

وَمَا خَلَقْنَا ٱلسَّمَآءَ وَٱلْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا بَٰطِلًاۚ ذَٰلِكَ ظَنُّ ٱلَّذِينَ
كَفَرُواْۚ فَوَيْلٌ لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنَ ٱلنَّارِ ٢٧ أَمْ نَجْعَلُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ
ٱلصَّٰلِحَٰتِ كَٱلْمُفْسِدِينَ فِي ٱلْأَرْضِ أَمْ نَجْعَلُ ٱلْمُتَّقِينَ كَٱلْفُجَّارِ
٢٨ كِتَٰبٌ أَنزَلْنَٰهُ إِلَيْكَ مُبَٰرَكٌ لِّيَدَّبَّرُوٓاْ ءَايَٰتِهِۦ وَلِيَتَذَكَّرَ أُوْلُواْ
ٱلْأَلْبَٰبِ ٢٩ وَوَهَبْنَا لِدَاوُۥدَ سُلَيْمَٰنَۚ نِعْمَ ٱلْعَبْدُ إِنَّهُۥٓ أَوَّابٌ
٣٠ إِذْ عُرِضَ عَلَيْهِ بِٱلْعَشِيِّ ٱلصَّٰفِنَٰتُ ٱلْجِيَادُ ٣١ فَقَالَ إِنِّيٓ أَحْبَبْتُ
حُبَّ ٱلْخَيْرِ عَن ذِكْرِ رَبِّي حَتَّىٰ تَوَارَتْ بِٱلْحِجَابِ ٣٢ رُدُّوهَا عَلَيَّۖ
فَطَفِقَ مَسْحًۢا بِٱلسُّوقِ وَٱلْأَعْنَاقِ ٣٣ وَلَقَدْ فَتَنَّا سُلَيْمَٰنَ
وَأَلْقَيْنَا عَلَىٰ كُرْسِيِّهِۦ جَسَدًا ثُمَّ أَنَابَ ٣٤ قَالَ رَبِّ ٱغْفِرْ لِي وَهَبْ
لِي مُلْكًا لَّا يَنۢبَغِي لِأَحَدٍ مِّنۢ بَعْدِيٓۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلْوَهَّابُ ٣٥
فَسَخَّرْنَا لَهُ ٱلرِّيحَ تَجْرِي بِأَمْرِهِۦ رُخَآءً حَيْثُ أَصَابَ ٣٦ وَٱلشَّيَٰطِينَ
كُلَّ بَنَّآءٍ وَغَوَّاصٍ ٣٧ وَءَاخَرِينَ مُقَرَّنِينَ فِي ٱلْأَصْفَادِ ٣٨ هَٰذَا
عَطَآؤُنَا فَٱمْنُنْ أَوْ أَمْسِكْ بِغَيْرِ حِسَابٍ ٣٩ وَإِنَّ لَهُۥ عِندَنَا لَزُلْفَىٰ وَحُسْنَ
مَـَٔابٍ ٤٠ وَٱذْكُرْ عَبْدَنَآ أَيُّوبَ إِذْ نَادَىٰ رَبَّهُۥٓ أَنِّي مَسَّنِيَ ٱلشَّيْطَٰنُ
بِنُصْبٍ وَعَذَابٍ ٤١ ٱرْكُضْ بِرِجْلِكَۖ هَٰذَا مُغْتَسَلٌۢ بَارِدٌ وَشَرَابٌ ٤٢



**(27) Ba mu halicci sama da qasa ba saboda wasa, wannan shi ne zaton waxanda suka kafirta, to azaba ta tabbata ga waxannan kafirai waxanda suke wannan zato, azabar wuta a ranar alqiyama, idan sun mutu a kan abin da suke kai na kafirci da mummunan zato ga Allah. (28) Ba zamu tava sanya waxanda suka yi imani da Allah, suka bi Manzonsa, kuma suka yi ayyuka nagari, su zama kamar masu yin varna a bayan qasa ta hanyar yin kafirci da savo ba. Kuma ba zamu sanya masu tsoron Ubangijinsu ta hanyar aikata umarninsa, da nisantar haninsa tamkar kafirai da munafikai waxanda suka nutse cikin savon Allah, lallai daidaita tsakaninsu zalunci ne, bai dace da Allah ba. kaxai dai Allah yana sakawa muminai masu tsoronsa, da shiga gidan Aljannah, kuma zai yi uquba ga kafirai shaqiyyai da shiga wuta, domin ba xaya suke a wurin Allah ba, kuma sakamakonsu ba zai yi daidai a wurin Allah ba. (29) Tabbas wannan Alqur'ani littafi ne da muka saukar da shi gare ka, mai yawan alheri da amfani, don mutane su yi tuntuntuni a cikin ma'anoninsa, kuma masu hankali su wa'azantu da shi. (30) Mun yi wa Annabi Dawud kyautar xan sa Sulaiman, wannan baiwa ce daga gare mu, da kuma alfarma don idonsa ya yi sanyi. Madallah da bawa Sulaiman, Haqiqa shi mai yawan tuba ne, da komawa ga Allah. (31) Ka tuna lokacin da aka bijiro masa da ingarmun dawakai, masu asali da gudu, a lokacin la'asar, suna tsayawa a kan qafafuwan su uku, suna xage ta huxun. Ba a gushe ba ana ta bijiro masa da waxannan dawakai har sai da rana ta faxi. (32) Sai Sulaiman ya ce: "Tabbas ni na fifita son dukiya – daga cikinka akwai son dawakai – a kan ambaton Ubangijina har rana ta fadi, na makara ban yi sallar la'asar ba. (33) Ku dawo min da waxannan dawakai, sai suka dawo masa da su, sai yasa takobi ya riqa sare musu qafafuwa da wuya. (34) Haqiqa mun jarrabi Annabi Sulaiman, mun sanya masa shaixani a kan gadon mulkinsa, wanda ya yi kama da mutum, ya yi tasarrufi a mulkinsa na xan wani lokaci taqaitacce, sannan ya dawowa da Annabi Sulaiman mulkinsa, kuma ya ba shi cikakkiyar dama a kan shaixanu. (35) Annabi Sulaiman ya ce: "Ya Ubangiji, ka gafarta min zunubaina, kuma ka ba ni mulki wanda ya kevanta da ni, kuma ya zama babu wanda yake da irinsa a bayana. Haqiqa kai - Ya Ubangijina mai yawan kyauta ne, mai babbar baiwa. (36) Sai muka amsa masa, muka hore masa iska, tana jayuwa ga umarninsa, kuma iska ce mai taushi, babu girgiza a cikinta, tare da haka tana gudu da qarfi, tana xaukan Annabi Sulaiman zuwa inda yake so. (37) Muka hore masa shaixanu, suna bin umarninsa. Daga cikinsu akwai magina, akwai masu nutso, waxanda suke yin nutso a cikin tekuna, su fito da abubuwa masu tsada daga cikinsu.**

**(38) Daga cikin shaixanun akwai kangararru, su ma an hore masa su, suna xaure a cikin sasari, ba sa iya ko motsawa.**

**(39) Ya kai Sulaiman wannan kyautarmu ce, wadda muka ba ka, domin amsa abin da ka nema, don haka ka ba wa wanda ka ga dama, ka hana wanda ka ga dama, ba za a yi maka hisabi a kan bayarwa ko hanawa ba.**

**(40) Tabbas Annabi Sulaiman yana cikin makusanta a wurinmu, kuma yana da kyakkyawar makoma da zai koma zuwa gare ta, ita ce Aljannah. (41) Ya kai wannan Manzo, ka ambaci bawan mu Annabi Ayyub, yayin da ya kira Allah Ubangijinsa ya ce: "Shaixan ya shafe ni da lamari mai wahalarwa da kuma azabtarwa".**

**(42) Sai muka ce da shi: "Ka daki qasa da qafarka" sai ya daki qasa da kafarsa, sai wani ruwa ya vuvvugo masa, yana sha yana wanka da shi, sai abin da yake tare da shi na cuta da rashin lafiya ya tafi.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Kwaxaitarwa a kan tunani da lura da ayoyin Alqur'ani. 2 - A cikin ayoyin akwai hujja a kan cewa daidai gwargwadon kuvutar zuciya da kaifin fahimtar xan adam, daidai gwargwadon yadda zai samu wa'azantuwa da amfanuwa da Alqur'ani mai girma. 3 - A cikin ayoyin akwai dalili da take nuna ingancin sananniyar qa'idar nan mai cewa: Duk wand ya bar wani abu saboda Allah, to Allah zai canza masa da wanda ya fi shi alheri.**

وَوَهَبْنَا لَهُۥٓ أَهْلَهُۥ وَمِثْلَهُم مَّعَهُمْ رَحْمَةً مِّنَّا وَذِكْرَىٰ لِأُو۟لِى ٱلْأَلْبَٰبِ
٤٣ وَخُذْ بِيَدِكَ ضِغْثًا فَٱضْرِب بِّهِۦ وَلَا تَحْنَثْ ۗ إِنَّا وَجَدْنَٰهُ صَابِرًا ۚ نِّعْمَ
ٱلْعَبْدُ ۖ إِنَّهُۥٓ أَوَّابٌ ٤٤ وَٱذْكُرْ عِبَٰدَنَآ إِبْرَٰهِيمَ وَإِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ أُو۟لِى
ٱلْأَيْدِى وَٱلْأَبْصَٰرِ ٤٥ إِنَّآ أَخْلَصْنَٰهُم بِخَالِصَةٍ ذِكْرَى ٱلدَّارِ ٤٦
وَإِنَّهُمْ عِندَنَا لَمِنَ ٱلْمُصْطَفَيْنَ ٱلْأَخْيَارِ ٤٧ وَٱذْكُرْ إِسْمَٰعِيلَ
وَٱلْيَسَعَ وَذَا ٱلْكِفْلِ ۖ وَكُلٌّ مِّنَ ٱلْأَخْيَارِ ٤٨ هَٰذَا ذِكْرٌ ۚ وَإِنَّ لِلْمُتَّقِينَ
لَحُسْنَ مَـَٔابٍ ٤٩ جَنَّٰتِ عَدْنٍ مُّفَتَّحَةً لَّهُمُ ٱلْأَبْوَٰبُ ٥٠ مُتَّكِـِٔينَ
فِيهَا يَدْعُونَ فِيهَا بِفَٰكِهَةٍ كَثِيرَةٍ وَشَرَابٍ ٥١ ۞ وَعِندَهُمْ قَٰصِرَٰتُ (نصف الحزب ٤٦)
ٱلطَّرْفِ أَتْرَابٌ ٥٢ هَٰذَا مَا تُوعَدُونَ لِيَوْمِ ٱلْحِسَابِ ٥٣ إِنَّ هَٰذَا
لَرِزْقُنَا مَا لَهُۥ مِن نَّفَادٍ ٥٤ هَٰذَا ۚ وَإِنَّ لِلطَّٰغِينَ لَشَرَّ مَـَٔابٍ
٥٥ جَهَنَّمَ يَصْلَوْنَهَا فَبِئْسَ ٱلْمِهَادُ ٥٦ هَٰذَا فَلْيَذُوقُوهُ حَمِيمٌ
وَغَسَّاقٌ ٥٧ وَءَاخَرُ مِن شَكْلِهِۦٓ أَزْوَٰجٌ ٥٨ هَٰذَا فَوْجٌ
مُّقْتَحِمٌ مَّعَكُمْ ۖ لَا مَرْحَبًۢا بِهِمْ ۚ إِنَّهُمْ صَالُوا۟ ٱلنَّارِ ٥٩ قَالُوا۟
بَلْ أَنتُمْ لَا مَرْحَبًۢا بِكُمْ ۖ أَنتُمْ قَدَّمْتُمُوهُ لَنَا ۖ فَبِئْسَ ٱلْقَرَارُ ٦٠
قَالُوا۟ رَبَّنَا مَن قَدَّمَ لَنَا هَٰذَا فَزِدْهُ عَذَابًا ضِعْفًا فِى ٱلنَّارِ ٦١



**(43) Sai muka amsa masa, muka yaye masa abin da yake damunsa na cuta, muka ba shi iyalansa, kuma muka qara masa kamarsu daga 'ya'ya da jikoki, don jin qan mu gare shi, da sakayya a kan haqurin da ya yi, kuma domin masu hankali su fahimci qarshen haquri shi ne yayewar baqin ciki, da samun lada. (44) Lokacin da Annabi Ayyub ya yi fushi da matarsa, ya yi rantsuwa sai ya doke ta bulala xari, sai muka ce masa: "Ya kai Ayyub ka xauki damin ciyawa ka doki matarka da shi, don ka warware rantsuwar da ka yi, kuma don kada ka karya rantsuwar da ka yi. Sai ya xauki damin ciyawa ya doke ta da shi. Haqiqa mun same shi mai haquri matuqa a kan jarrabawar da muka yi masa, madallah da bawa Ayyuba, lallai shi mai yawan komawa ne ga Allah. (45) Ya kai wannan Manzo ka tuna bayin mu waxanda muka zave su, da Manzannin mu waxanda muka aiko su: Ibrahim, da Ishaq da Yaqub, duk sun kasance masu qarfi ne a cikin xa'ar Allah da neman yardar sa, kuma masu matuqar basira ne a kan gaskiya. (46) Haqiqa mun yi musu baiwa da wata kevantacciyar baiwa, ita ce: raya zukatansu da tuna lahira, da yi mata tanadi da aiki nagari, da kiran mutane zuwa ga aiki don lahira. (47) Tabbas su, suna cikin waxanda muka zave su, don yi mana xa'a da bautar mu, kuma muka zave su don xaukar nauyin sakonmu, da isar da shi ga mutane. (48) Ya kai wannan Annabi, ka tuna Annabi Isma'il xan Annabi Ibrahim, kuma ka tuna Alyasa'u, ka tuna Zul-kiflu, ka yi musu yabo ma fi kyau, domin sun cacanci hakan. Dukkan waxannan suna cikin zavavvu a wurin Allah. (49) Wannan ambato ne mai kyau na waxannan a cikin Alqur'ani. Waxanda suke jin tsoron Allah ta hanyar kamanta umarnin Allah da nisantar abubuwan da ya hana, suna da makoma mai kyau a gidan lahira. (50) Wannan makoma mai kyau ita ce Aljannatai na dindindin, da za su shige su ranar alqiyama, an buxe musu kofofin ta don murna da zuwan su. (51) Zasu kishingixa a kan gadajensu, waxanda aka yi masu ado, suna umartar masu yi musu hidima su kawo musu abin da suke sha'awa na kayan marmari masu yawa, kuma iri-iri, haka ma abin sha, irin wanda suke sha'awa, na giya da waninta. (52) A tare da su akwai mataye da suka taqaita ganinsu a kan mazajensu kaxai, basa qetarewa zuwa waninsu, kuma tsarekun juna ne a shekaru. (53) Wannan shi ne alqawarin da aka yi muku – Ya ku masu jin tsoron Allah - na daddaxan sakamako ranar alqiyama a kan ayyukanku na qwarai da kuka kasance kuna aikatawa a duniya. (54) Tabbas wannan abin da muka ambata na sakamako, arziki ne da muke azurta masu tsoron Allah da shi a ranar alqiyama, kuma arziki ne mai xorewa, baya yankewa ko ya qare. (55) Wanna abin da muka ambata shi ne sakamakon masu jin tsoron Allah. Waxanda suka qetare iyakokin Allah ta hanyar kafirci da savo, suna da wani sakamako da ya sha bamban da sakamakon masu tsoron Allah, suna da mummunar makoma da zasu koma gare ta a ranar alqiyama. (56) Wannan sakamako shi ne wutar Jahannama da zata kewaye su, zasu sha fama da zafinta da yadda take ci bal-bal, suna da wata shimfixa a cikinta, tir da shimfixa irin wannan shimfixar ta su. (57) Wannan azabar ruwa ne mai matuqar zafi, da ruwan da yake kwararowa daga jikin 'yan wuta, waxanda ake azabtarwa a cikin ta, don haka su sha shi, kuma shi ne abin shan su, wanda baya kawar da qishirwa. (58) Kuma suna da wata azaba ta daban, daga irin waxannan azabu, suna da azaba kala-kala da za a azabta su da su a ranar lahira. (59) Idan 'yan wuta suka shige ta, sai husuma da zage zage ya gudana a tsakaninsu, sashensu ya barranta da sashe, sai su ce musu: "Waxannan ma 'yan wuta ne za su shiga wuta tare da ku. Sai su basu amsa su ce: "Va a maraba da su, za su xanxani azabar wuta kamar yadda muma muke xanxana". (60) Sai dandazon mabiya su cewa jagororinsu: "Ku ne dai ba a maraba da ku – Ku jagorori shugabanni – ku ne kuka janyo mana wannan azaba mai raxaxi, saboda vatar da mu da kuka yi, tir da wannan matabbata, matabbatar su gaba xaya wadda ita ce wuta. (61) Sai mabiya su ce: "Ya ubangijin mu, duk wanda ya vatar da mu ga barin shiriya, bayan ta zo mana, ka sanya azabarsa a wuta ta zama ninkin ba ninkin".**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Duk wanda ya yi haquri a kan wata cuta, to Allah zai saka masa da lada mai yawa, a duniya ko a lahira. kuma ya amsa addu'arsa idan ya yi. 2 - A cikin ayoyin akwai dalili a kan halaccin miji ya doki matarsa, don ladabtarwa, duka ba mai cutarwa ba, don Annabi Ayyuba ya rantse sai ya doki matarsa, kuma ya aikata.**

وَقَالُواْ مَا لَنَا لَا نَرَىٰ رِجَالٗا كُنَّا نَعُدُّهُم مِّنَ ٱلۡأَشۡرَارِ ٦٢ أَتَّخَذۡنَٰهُمۡ
سِخۡرِيًّا أَمۡ زَاغَتۡ عَنۡهُمُ ٱلۡأَبۡصَٰرُ ٦٣ إِنَّ ذَٰلِكَ لَحَقّٞ تَخَاصُمُ أَهۡلِ
ٱلنَّارِ ٦٤ قُلۡ إِنَّمَآ أَنَا۠ مُنذِرٞۖ وَمَا مِنۡ إِلَٰهٍ إِلَّا ٱللَّهُ ٱلۡوَٰحِدُ ٱلۡقَهَّارُ ٦٥
رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَا ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡغَفَّٰرُ ٦٦ قُلۡ هُوَ نَبَؤٌاْ
عَظِيمٌ ٦٧ أَنتُمۡ عَنۡهُ مُعۡرِضُونَ ٦٨ مَا كَانَ لِيَ مِنۡ عِلۡمِۭ بِٱلۡمَلَإِ ٱلۡأَعۡلَىٰٓ
إِذۡ يَخۡتَصِمُونَ ٦٩ إِن يُوحَىٰٓ إِلَيَّ إِلَّآ أَنَّمَآ أَنَا۠ نَذِيرٞ مُّبِينٌ ٧٠ إِذۡ قَالَ
رَبُّكَ لِلۡمَلَٰٓئِكَةِ إِنِّي خَٰلِقُۢ بَشَرٗا مِّن طِينٖ ٧١ فَإِذَا سَوَّيۡتُهُۥ وَنَفَخۡتُ
فِيهِ مِن رُّوحِي فَقَعُواْ لَهُۥ سَٰجِدِينَ ٧٢ فَسَجَدَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ كُلُّهُمۡ
أَجۡمَعُونَ ٧٣ إِلَّآ إِبۡلِيسَ ٱسۡتَكۡبَرَ وَكَانَ مِنَ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٧٤ قَالَ
يَٰٓإِبۡلِيسُ مَا مَنَعَكَ أَن تَسۡجُدَ لِمَا خَلَقۡتُ بِيَدَيَّۖ أَسۡتَكۡبَرۡتَ أَمۡ كُنتَ
مِنَ ٱلۡعَالِينَ ٧٥ قَالَ أَنَا۠ خَيۡرٞ مِّنۡهُ خَلَقۡتَنِي مِن نَّارٖ وَخَلَقۡتَهُۥ مِن طِينٖ
٧٦ قَالَ فَٱخۡرُجۡ مِنۡهَا فَإِنَّكَ رَجِيمٞ ٧٧ وَإِنَّ عَلَيۡكَ لَعۡنَتِيٓ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلدِّينِ
٧٨ قَالَ رَبِّ فَأَنظِرۡنِيٓ إِلَىٰ يَوۡمِ يُبۡعَثُونَ ٧٩ قَالَ فَإِنَّكَ مِنَ
ٱلۡمُنظَرِينَ ٨٠ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡوَقۡتِ ٱلۡمَعۡلُومِ ٨١ قَالَ فَبِعِزَّتِكَ
لَأُغۡوِيَنَّهُمۡ أَجۡمَعِينَ ٨٢ إِلَّا عِبَادَكَ مِنۡهُمُ ٱلۡمُخۡلَصِينَ ٨٣



**(62) Masu girman kai da xagawa suka ce: "Yaya ba ma ganin wasu mutane a wuta, waxanda a duniya muna tsammaninsu a cikin shaqiyyai waxanda suka cancanci azaba?".**

**(63) Shin izgilin da muke yi musu kuskure ne, ba su cancanci azaba ba, ko kuwa izgilin da muke musu daidai ne, sun shiga wutar, idanuwan mu ne basu kai gare su ba.**

**(64) Tabbas wannan abin da muka ambata na husumar kafirai a tsakaninsu a ranar alqiyama gaskiya ne, babu wani kokwanto ko shakka a ciki.**

**(65) Ya Muhammad ka cewa kafirai daga cikin mutanenka: " Kaxai ni mai gargaxi ne a gare ku daga azabar Allah, kada ya saukar muku da ita saboda kafircewarku da shi, da qaryata Manzanninsa, babu wani abin bauta da ya cancanta a bauta masa sai Allah mai tsarki, shi kaxa ne a cikin girmansa da siffofinsa da sunayensa, shi ne mai rinjayen da ya rinjayi dukkan komai, komai mai rankwafawa ne a gare shi.**
**(66) Shi ne Ubangijin sammai, Ubangijin qassai, Ubangijin abin da yake tsakaninsu, kuma shi ne Mabuwayi a cikin mulkinsa, babu mai rinjayarsa. Shi ne mai yawan gafarta zunuban masu tuba daga cikin bayinsa.**

**(67) Ya kai wannan Manzo ka cewa waxannan masu qaryatawar: "Tabbas Alkur'ani labari ne mai matukar girma".**

**(68) "Amma ku kuna bijirewa wannan labari mai girma, ba kwa lura da shi".**

**(69) Ba ni da wani ilimi game da zancen da yake gudana a tsakanin Mala'iku dangane da halittar Annabi Adam, ba don Allah ya yi min wahayi, kuma ya sanar da ni ba.**

**(70) Kaxai dai Allah yana min wahayi ne, domin ni mai gargaxi ne a gare ku, kuma mai bayyana gargaxin.**

**(71) Ka tuna lokacin da Ubangijinka ya cewa Mala'iku: "Tabbas ni zan halicci mutum daga tavo" shi ne Adam (A.S).**
**(72) To idan na daidaita halittarsa, na gyara kamanninsa, na busa masa daga ruhi na, to ku yi masa sujjada.**

**(73) Sai Mala'iku suka aikata umarnin Ubangijinsu, suka yi sujjada ta girmamawa gaba xayansu, babu wanda ya rage a cikinsu, face sai da ya yi sujjada ga Adam.**

**(74) Sai Iblisu, shi ya yi girman kai ga yin sujjada, don haka ya kasance daga cikin kafirai saboda wannan girman kan.**

**(75) Sai Allah ya ce: "Ya kai Iblisu, me ya hana ka ka yi sujjada ga Adam, wanda na halicce shi da hannuna?. Shin girman kai ne ya hana ka, ko kuwa dama can kai mai girman kai ne da fankama ga Ubangijnka?.**

**(76) Sai Iblisu ya ce: "Ni na fi Adam alheri, domin ka halicce ni daga wuta, shi kuma ka halicce shi daga tavo". Shi Iblisu yana ganin wuta tafi tavo.**

**(77) Sai Allah ya cewa Iblisu: "Ka fita daga cikin Aljannah, kai tsinanne ne marar albarka".**

**(78) Kuma kai korarre ne daga Aljannah daga yau har zuwa ranar sakamako, ita ce ranar tashin alqiyama.**

**(79) Sai Iblisu ya ce: "To ka jinkirta min, kada ka kashe ni har zuwa ranar da zaka tashi bayinka".**

**(80) Sai Allah ya ce: " To, kai kana cikin waxanda za a jinkirta musu".**

**(81) Har zuwa ranar wani lokaci sananne, qayyadajje wanda za a halakar da kai.**

**(82) Sai Iblisu ya ce: "Ina yin rantsuwa da ikon ka da buwayarka, tabbas sai na vatar da 'ya'yan Adam gaba xaya".**

**(83) Sai dai wanda ka kare shi daga vatarwa ta, kuma ka tsarkake shi don bauta maka kai kaxai.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Yin ijtihadi ko qiyasi matuqar akwai nassi bayyananne (Aya ko hadisi) hanya ce vatacciya. 2 - Kafircin Iblis kafirci ne na girman kai da taurin kai. 3 - Waxanda Allah ya tsarkake su don bautarsa daga cikin halitta, to Shaixan ba shi da iko a kansa.**

قَالَ فَٱلۡحَقُّ وَٱلۡحَقَّ أَقُولُ ٨٤ لَأَمۡلَأَنَّ جَهَنَّمَ مِنكَ وَمِمَّن تَبِعَكَ مِنۡهُمۡ
أَجۡمَعِينَ ٨٥ قُلۡ مَآ أَسۡـَٔلُكُمۡ عَلَيۡهِ مِنۡ أَجۡرٖ وَمَآ أَنَا۠ مِنَ ٱلۡمُتَكَلِّفِينَ
٨٦ إِنۡ هُوَ إِلَّا ذِكۡرٞ لِّلۡعَٰلَمِينَ ٨٧ وَلَتَعۡلَمُنَّ نَبَأَهُۥ بَعۡدَ حِينِۭ ٨٨

آياتها ٧٥ سُورَةُ الزُّمَرِ ترتيبها ٣٩

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

تَنزِيلُ ٱلۡكِتَٰبِ مِنَ ٱللَّهِ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡحَكِيمِ ١ إِنَّآ أَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ
ٱلۡكِتَٰبَ بِٱلۡحَقِّ فَٱعۡبُدِ ٱللَّهَ مُخۡلِصٗا لَّهُ ٱلدِّينَ ٢ أَلَا
لِلَّهِ ٱلدِّينُ ٱلۡخَالِصُۚ وَٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِهِۦٓ أَوۡلِيَآءَ
مَا نَعۡبُدُهُمۡ إِلَّا لِيُقَرِّبُونَآ إِلَى ٱللَّهِ زُلۡفَىٰٓ إِنَّ ٱللَّهَ يَحۡكُمُ
بَيۡنَهُمۡ فِي مَا هُمۡ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي مَنۡ هُوَ
كَٰذِبٞ كَفَّارٞ ٣ لَّوۡ أَرَادَ ٱللَّهُ أَن يَتَّخِذَ وَلَدٗا لَّٱصۡطَفَىٰ
مِمَّا يَخۡلُقُ مَا يَشَآءُۚ سُبۡحَٰنَهُۥۖ هُوَ ٱللَّهُ ٱلۡوَٰحِدُ ٱلۡقَهَّارُ
٤ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ بِٱلۡحَقِّۖ يُكَوِّرُ ٱلَّيۡلَ عَلَى
ٱلنَّهَارِ وَيُكَوِّرُ ٱلنَّهَارَ عَلَى ٱلَّيۡلِۖ وَسَخَّرَ ٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَۖ
كُلّٞ يَجۡرِي لِأَجَلٖ مُّسَمًّىۗ أَلَا هُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡغَفَّٰرُ ٥



(84) Sai Allah Maxaukakin sarki ya ce: "Ita dai gaskiya daga gare ni take, kuma abin da nake faxa gaskiya ne, ba zan tava faxar waninta ba".

(85) Wallahi ranar alqiyama sai na cika wuta da kai, da duk wanda ya bi ka a cikin kafircinka, daga 'ya'yan Adam gaba xaya.

(86) Ya kai wannan Manzo ka cewa waxannan mushirikai: "Ba na tambayarku wani lada a kan nasihar da nake yi muku, kuma ni bana cikin masu qaqalen faxar abin da ba a umarce ni ba da shi ba".

(87) Alqur'ani ba wani abu ba ne face tunatar da waxanda shari'a ta hau kansu daga cikin mutane da aljannu.

(88) Kuma tabbas da sannu zaku san labarin wannan Alqur'ani, cewa shi gaskiya ne, bayan wani lokaci na nan kusa, a yayin da kuka mutu.

# Suratuz Zumar

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Kira zuwa ga kaxaita Allah da tsarkake ibada gare shi, da watsar da shirka, da kuma bayanin qarshen kowanne a lahira.**

## Tafsir:

**(1) Saukar da Alqur'ani daga Allah ne Mabuwayi, wanda babu wanda ya isa ya rinjaye shi, kuma shi ne mai hikima cikin gudanarwar sa, da halittar sa, da shari'ar sa. Babu wanda ya saukar da shi wanda ba Allah ba.**

**(2) Ya kai wannan Manzo, haqiqa mun saukar maka da Alqur'ani, wanda ya qunshi gaskiya, labaran da suke cikinsa duk gaskiya ne, hukunce-hukuncensa duk adalci ne, don haka ka bautawa Allah kana mai kaxaita shi, kana mai tsarkake tauhidin ka daga shirka.**

**(3) Ku saurara, addinin da babu shirka a cikinsa na Allah ne. Waxanda suka riqi wasu majivinta lamari daga cikin gumaka da xagutai, suna bauta musu koma bayan Allah, suna bada uzuri a kan bautarsu da cewa: "Ba ma bautawa waxannan sai don su kusantar da mu ga Allah da wani matsayi, su xaga buqatun mu zuwa gare shi, su cece mu a wurinsa". Tabbas Allah zai yi hukunci tsakanin muminai masu kaxaita Allah, da kafirai masu shirka a ranar alqiyama, cikin abin da suka kasance suna yin savani game da shi na kaxaita Allah. Tabbas Allah baya datar da mai yi masa qarya, ta hanyar jingina masa abokin tarayya zuwa ga gaskiya, mai yawan butulcewa ni'imominsa.**

**(4) Da Allah ya so ya riqi xa, to da ya zavi abin da ya ga dama daga cikin halittarsa, ya sanya shi a matsayin xa'a. Allah ya tsarkaka kuma ya girmama daga abin da waxannan mushirikai suke faxa. Allah shi ne tilo a zatinsa da siffofinsa da ayyukansa, ba shi da abokin tarayya a cikinsu, kuma shi ne mai rinjaye a kan bayinsa gaba xaya.**

**(5) Ya halicci sammai da qassai saboda wata hikima mai muhimmanci, ba wai don wasa ba kamar yadda azzalumai suke faxa. yana shigar da dare a cikin yini, kuma yana shigar da yini a cikin dare, idan xaya ya zo sai xayan ya vace, kuma ya hore rana, ya hore wata, kowanne daga cikinsu yana gudana a iya wani lokaci da aka qaddara shi, shi ne qarewar wannan rayuwar ta duniya. Ku saurara, Allah shi ne mai tsarki, kuma Mabuwayi, wanda yake kama maqiyansa, babu wanda yake galaba a kansa, mai yawan gafarta zunuban wanda ya tuba daga cikin bayinsa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Mai kira zuwa ga Allah yana neman ladansa ne a wurin Allah kaxai, baya neman lada a wurin mutanen da yake kiran su zuwa ga gaskiya.**

**2 - Kallafa kai abin da ba nema ba baya daga cikin addini.**

**3 - Yin tawassuli wurin Allah yana kasancewa ne ta hanyar sunayensa, da siffofinsa, da imani, da ayyuka nagari kawai.**

خَلَقَكُم مِّن نَّفۡسٖ وَٰحِدَةٖ ثُمَّ جَعَلَ مِنۡهَا زَوۡجَهَا وَأَنزَلَ لَكُم
مِّنَ ٱلۡأَنۡعَٰمِ ثَمَٰنِيَةَ أَزۡوَٰجٖۚ يَخۡلُقُكُمۡ فِي بُطُونِ أُمَّهَٰتِكُمۡ
خَلۡقٗا مِّنۢ بَعۡدِ خَلۡقٖ فِي ظُلُمَٰتٖ ثَلَٰثٖۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمۡ لَهُ
ٱلۡمُلۡكُۖ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ فَأَنَّىٰ تُصۡرَفُونَ ٦ إِن تَكۡفُرُواْ فَإِنَّ
ٱللَّهَ غَنِيٌّ عَنكُمۡۖ وَلَا يَرۡضَىٰ لِعِبَادِهِ ٱلۡكُفۡرَۖ وَإِن تَشۡكُرُواْ يَرۡضَهُ
لَكُمۡۗ وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٞ وِزۡرَ أُخۡرَىٰۗ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُم مَّرۡجِعُكُمۡ
فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَۚ إِنَّهُۥ عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ٧
ثلاثة أرباع الحزب ٤٦ ۞وَإِذَا مَسَّ ٱلۡإِنسَٰنَ ضُرّٞ دَعَا رَبَّهُۥ مُنِيبًا إِلَيۡهِ ثُمَّ إِذَا خَوَّلَهُۥ نِعۡمَةٗ
مِّنۡهُ نَسِيَ مَا كَانَ يَدۡعُوٓاْ إِلَيۡهِ مِن قَبۡلُ وَجَعَلَ لِلَّهِ أَندَادٗا لِّيُضِلَّ
عَن سَبِيلِهِۦۚ قُلۡ تَمَتَّعۡ بِكُفۡرِكَ قَلِيلًا إِنَّكَ مِنۡ أَصۡحَٰبِ ٱلنَّارِ ٨
أَمَّنۡ هُوَ قَٰنِتٌ ءَانَآءَ ٱلَّيۡلِ سَاجِدٗا وَقَآئِمٗا يَحۡذَرُ ٱلۡأٓخِرَةَ
وَيَرۡجُواْ رَحۡمَةَ رَبِّهِۦۗ قُلۡ هَلۡ يَسۡتَوِي ٱلَّذِينَ يَعۡلَمُونَ وَٱلَّذِينَ
لَا يَعۡلَمُونَۗ إِنَّمَا يَتَذَكَّرُ أُوْلُواْ ٱلۡأَلۡبَٰبِ ٩ قُلۡ يَٰعِبَادِ ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ رَبَّكُمۡۚ لِلَّذِينَ أَحۡسَنُواْ فِي هَٰذِهِ ٱلدُّنۡيَا حَسَنَةٞۗ
وَأَرۡضُ ٱللَّهِ وَٰسِعَةٌۗ إِنَّمَا يُوَفَّى ٱلصَّٰبِرُونَ أَجۡرَهُم بِغَيۡرِ حِسَابٖ ١٠



**(6) Ubangijinku ya halicce ku – Ya ku mutane - daga rai guda xaya shi ne Annabi Adam, sannan ya halicci matarsa Hauwa'u daga gare shi, sannan ya halitta muku daga raquma da shanu da tumakai da awaki, dangi takwas, daga kowane dangi ya halicci namiji da mace. Ubangijinku yana halittar ku a cikin ciki iyayen ku mata, mataki bayan mataki, cikin duhun ciki da na mahaifa da na mabiyiya, wanda yake halittar wannan gaba xaya shi ne Allah Ubangijinku, mulki nasa ne shi kaxai, babu abin bautawa da gaskiya sai shi, to ta yaya kuke karkacewa daga bauta masa, zuwa bautawa waxanda baya halittar komai, alhali su ne ake halitta?.**

**(7) Ya ku mutane, idan kun kafircewa Ubangijinku, to ku sani Allah Mawadaci ne ga barin imaninku, kafircinku ba zai cutar da shi ba, cutarwar kafircin ku kanku zata koma, kuma Allah bai yarda bayinsa su kafirce masa ba, kuma baya umartar su da kafirci, saboda Allah baya umarni da alfasha da munkari. Idan zaku godewa Allah akan ni'imar da ya yi muku, kuma ku yi imani da shi, to zai yarda da godiyar ku, ya baku lada, wata rai bata xaukan zunubin wata rai daban, a'a kowace rai tana rataye da abin da ta aikata, sannan zuwa ga Ubangijinku shi kaxai makomarku zata kasance ranar alqiyama, ya baku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa a duniya, ya yi muku sakayya a kan ayyukanku, haqiqa shi mai tsarki ne, kuma masanin abin da ke cikin zukatan bayinsa, babu abin da yake vuya a gare shi.**

**(8) Idan wani abu ya samu kafiri, na rashin lafiya ko rashin dukiya, ko tsoron nutsewa, sai ya kira Ubangijinsa a kan ya yaye masa abin da yake tare da shi na cuta, yana mai komawa zuwa gare shi, shi kaxai. Idan ya yi masa ni'ima ya yaye masa cutar da ta same shi, sai ya bar abin da yake kai a baya na qasqantar da kai zuwa ga Allah, sai ya sanyawa Allah abokan tarayya, yana bauta musu koma bayansa, don ya kawar da waninsa daga hanyar da take kaiwa zuwa ga Allah. To ka cewa wanda wannan ne halinsa – Ya kai wannan Manzo -: "Ka ji daxi da kafircinka cikin abin da ya rage a rayuwarka, lokaci ne kaxan, haqiqa kai kana cikin ma'abota wuta, waxanda za su lazimce ta ranar alqiyama, irin yadda aboki yake lazimtar abokinsa.**

**(9) Yanzu wanda yake bin Allah, yana qare lokutansa cikan dare yana mai sujjada ga Ubangijinsa, yana mai tsayuwa gare shi, yana tsoron azabar lahira, yana fatan samun rahamar Ubangijinsa, shi ya fi alheri ko wancan kafirin da yake bautawa Allah a lokacin tsanani, ya kafirce masa a lokacin yalwa, ya sanya masa abokan tarayya?. Ka ce – Ya kai wannan Manzo – shin wanda suka san abin da Allah ya wajabta musu, saboda saninsu ga Allah, zasu yi daidai da waxancan da basu san komai ba daga wannan?. Kaxai masu lafiyayyun hankula ne suke sani bambancin waxannan vangarori guda biyu.**

**(10) Ya kai wannan Manzo ka cewa bayina waxanda suka yi imani da ni, da Manzanni na: "Ku ji tsoron Ubangijinku, ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana. Waxanda suka kyautata aiki a cikinku a duniya suna da kyakkyawa a duniya, na samun nasara da lafiya da dukiya, a lahira kuma suna da Aljannah. Qasar Allah mai yalwa ce, ku yi hijira a cikinta, har ku samu wurin da zaku bautawa Allah a cikinta, babu abin da zai hana ku. Ana ba wa masu haquri ladansu ranar alqiyama ba tare da qirgawa ko qaddarawa ba, saboda yawansa da kala-kalansa.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Kulawar da Allah yake yi wa mutum lokacin yana cikin mahaifiyarsa. 2 - Tabbatar da siffar wadata ga Allah, da siffar yarda. 3 - Kafuri yana nufar Allah a lokacin tsanani, kuma ya bijire masa a lokacin yalwa, kuma wannan yana nuna cewa harigido kawai yake yi. 4 - Tsoro da kwaxayi siffofi ne guda biyu cikin siffofin masu imani.**

قُلۡ إِنِّيٓ أُمِرۡتُ أَنۡ أَعۡبُدَ ٱللَّهَ مُخۡلِصٗا لَّهُ ٱلدِّينَ ١١ وَأُمِرۡتُ لِأَنۡ أَكُونَ
أَوَّلَ ٱلۡمُسۡلِمِينَ ١٢ قُلۡ إِنِّيٓ أَخَافُ إِنۡ عَصَيۡتُ رَبِّي عَذَابَ يَوۡمٍ عَظِيمٖ
١٣ قُلِ ٱللَّهَ أَعۡبُدُ مُخۡلِصٗا لَّهُۥ دِينِي ١٤ فَٱعۡبُدُواْ مَا شِئۡتُم مِّن دُونِهِۦۗ
قُلۡ إِنَّ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٱلَّذِينَ خَسِرُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ وَأَهۡلِيهِمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۗ
أَلَا ذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡخُسۡرَانُ ٱلۡمُبِينُ ١٥ لَهُم مِّن فَوۡقِهِمۡ ظُلَلٞ مِّنَ ٱلنَّارِ
وَمِن تَحۡتِهِمۡ ظُلَلٞۚ ذَٰلِكَ يُخَوِّفُ ٱللَّهُ بِهِۦ عِبَادَهُۥۚ يَٰعِبَادِ فَٱتَّقُونِ ١٦
وَٱلَّذِينَ ٱجۡتَنَبُواْ ٱلطَّٰغُوتَ أَن يَعۡبُدُوهَا وَأَنَابُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ لَهُمُ ٱلۡبُشۡرَىٰۚ
فَبَشِّرۡ عِبَادِ ١٧ ٱلَّذِينَ يَسۡتَمِعُونَ ٱلۡقَوۡلَ فَيَتَّبِعُونَ أَحۡسَنَهُۥٓۚ
أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ هَدَىٰهُمُ ٱللَّهُۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمۡ أُوْلُواْ ٱلۡأَلۡبَٰبِ ١٨
أَفَمَنۡ حَقَّ عَلَيۡهِ كَلِمَةُ ٱلۡعَذَابِ أَفَأَنتَ تُنقِذُ مَن فِي ٱلنَّارِ ١٩
لَٰكِنِ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَوۡاْ رَبَّهُمۡ لَهُمۡ غُرَفٞ مِّن فَوۡقِهَا غُرَفٞ مَّبۡنِيَّةٞ تَجۡرِي
مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ وَعۡدَ ٱللَّهِ لَا يُخۡلِفُ ٱللَّهُ ٱلۡمِيعَادَ ٢٠ أَلَمۡ تَرَ
أَنَّ ٱللَّهَ أَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَسَلَكَهُۥ يَنَٰبِيعَ فِي ٱلۡأَرۡضِ ثُمَّ
يُخۡرِجُ بِهِۦ زَرۡعٗا مُّخۡتَلِفًا أَلۡوَٰنُهُۥ ثُمَّ يَهِيجُ فَتَرَىٰهُ مُصۡفَرّٗا ثُمَّ
يَجۡعَلُهُۥ حُطَٰمًاۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَذِكۡرَىٰ لِأُوْلِي ٱلۡأَلۡبَٰبِ ٢١

**(11) Ya kai wannan Manzo ka ce: "Haqiqa Allah ya umarce ni in bauta masa shi kaxai, ina mai tsarkake ibada a gare shi".**
**(12) Kuma ya umarce ni in zama farkon wanda ya musulunta, ya miqa wuya, ya jayu zuwa gare shi, a cikin wannan al'umma".**
**(13) Ka ce – Ya kai wannan Manzo -: "Haqiqa ni ina jin tsoron in na savawa Allah, ban yi masa xa'a ba, ina jin tsoron azabar wata rana mai girma, ita ce ranar alqiyama".**
**(14) Ka ce – Ya kai wannan Manzo -: "Haqiqa ni ina bautawa Allah shi kaxai, ina mai tsarkake ibada a gare shi, ba na bautawa wani tare da shi".**
**(15) Ku bautawa abin da kuka ga dama – Ya ku mushirikai – koma bayan Allah, daga cikin gumaka (Wannan umarnin na jan kunne ne da tsoratarwa). Ka ce – Ya kai wannan Manzo –: "Haqiqanin masu asara su ne waxanda suka yi asarar kawunansu, suka yi asarar iyalansu, ba su haxu da su ba, saboda sun rabu da su, sun shiga Aljannah su kaxai, ko sun shiga wuta tare da su, ba za su haxu ba har abada. Ku saurara haqiqa wannan ita ce asara bayyananniya, babu kokwanto a cikinta" .**
**(16) Saman su hayaqi ne da bakin wuta da zafi, a qasan su ma hayaqi ne da bakin wuta da zafi. Wannan abin da aka ambata na azaba Allah yana tsoratar da bayinsa da shi. Ya ku bayina ku ji tsoro na, ta hanyar kamanta umarni na, da nisantar abubuwan da na hana.**
**Yayin da Allah ya ambaci halin da masu laifi za su shiga, sai ya ambaci halin da bayinsa nagari za su shiga ya ce:**
**(17) Waxanda suka nisanci bautar gumaka, da duk wani abin da ake bautawa koma bayan Allah, suka dawo zuwa ga Allah ta hanyar tuba, to suna da bushara da Aljannah yayin mutuwa, da a cikin qabari, da ranar alqiyama, don haka – Ya kai wannan Manzo – ka yi wa bayina bushara.**
**(18) Waxanda suke sauraron magana, suke bambance mai kyau da maras kyau daga cikin wannan magana, sai su bi mafi kyan zance, saboda abin da yake cikinsa na amfani, to waxannan masu waxancan siffofi su ne waxanda Allah ya datar da su zuwa ga shiriya, kuma waxannan su ne ma'abota lafiyayyun hankula.**
**(19) Wanda kalmar azaba ta wajaba a kansa, saboda ya ci gaba da kafircinsa da vatansa, to wannan baka da wata dabara – Ya kai wannan Manzo – wajen shiryar da shi, da datar da shi. Yanzu kai – Ya kai Manzo – zaka iya tseratar da wanda wannan ce siffarsa daga wuta?!".**
**(20) Amma waxanda suka ji tsoron Ubangijinsu, ta hanyar kamanta umarninsa da nisantar abubuwan da ya hana, to suna da masaukai maxaukaka, sashensu a kan sashe, qoramu suna gudana ta qarqashin su. Allah ya yi musu alqawari da haka, kuma Allah baya sava alqawari.**
**(21) Haqiqa ku kun sani, ta hanyar gani da ido, cewa Allah yana saukar da ruwan sama, sai ya shigar da shi cikin idanun ruwa da magudana, sannan sai ya fito da shuka kala-kala da wannan ruwa, sannan sai shukar ta bushe, sai ka gan ta kalarta ta koma ruwan xorawa, bayan da can tana kore shar, sannan sai Allah ya sanya ta bayan ta bushe ta karkarye ta zama karmami. Lallai a cikin wannan abin da aka ambata akwai tunatarwa ga masu rayayyun zukata.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Tsarkake ibada ga Allah sharaxi ne wajen karvar ta.**
**2 - Savon Allah yana wajabta saukar azabar Allah da fushinsa.**
**3 - Shiryarwa ta dace zuwa ga imani abu ne da yake hannun Allah, ba a hannun Manzon Allah (S.A.W) yake ba.**

أَفَمَن شَرَحَ ٱللَّهُ صَدۡرَهُۥ لِلۡإِسۡلَٰمِ فَهُوَ عَلَىٰ نُورٖ مِّن رَّبِّهِۦۚ فَوَيۡلٞ
لِّلۡقَٰسِيَةِ قُلُوبُهُم مِّن ذِكۡرِ ٱللَّهِۚ أُوْلَٰٓئِكَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٍ ٢٢
ٱللَّهُ نَزَّلَ أَحۡسَنَ ٱلۡحَدِيثِ كِتَٰبٗا مُّتَشَٰبِهٗا مَّثَانِيَ تَقۡشَعِرُّ مِنۡهُ
جُلُودُ ٱلَّذِينَ يَخۡشَوۡنَ رَبَّهُمۡ ثُمَّ تَلِينُ جُلُودُهُمۡ وَقُلُوبُهُمۡ
إِلَىٰ ذِكۡرِ ٱللَّهِۚ ذَٰلِكَ هُدَى ٱللَّهِ يَهۡدِي بِهِۦ مَن يَشَآءُۚ وَمَن
يُضۡلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِنۡ هَادٍ ٢٣ أَفَمَن يَتَّقِي بِوَجۡهِهِۦ سُوٓءَ
ٱلۡعَذَابِ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۚ وَقِيلَ لِلظَّٰلِمِينَ ذُوقُواْ مَا كُنتُمۡ تَكۡسِبُونَ
٢٤ كَذَّبَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ فَأَتَىٰهُمُ ٱلۡعَذَابُ مِنۡ حَيۡثُ
لَا يَشۡعُرُونَ ٢٥ فَأَذَاقَهُمُ ٱللَّهُ ٱلۡخِزۡيَ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۖ وَلَعَذَابُ
ٱلۡأٓخِرَةِ أَكۡبَرُۚ لَوۡ كَانُواْ يَعۡلَمُونَ ٢٦ وَلَقَدۡ ضَرَبۡنَا لِلنَّاسِ فِي
هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانِ مِن كُلِّ مَثَلٖ لَّعَلَّهُمۡ يَتَذَكَّرُونَ ٢٧ قُرۡءَانًا عَرَبِيًّا
غَيۡرَ ذِي عِوَجٖ لَّعَلَّهُمۡ يَتَّقُونَ ٢٨ ضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلٗا رَّجُلٗا فِيهِ
شُرَكَآءُ مُتَشَٰكِسُونَ وَرَجُلٗا سَلَمٗا لِّرَجُلٍ هَلۡ يَسۡتَوِيَانِ مَثَلًاۚ
ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِۚ بَلۡ أَكۡثَرُهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ ٢٩ إِنَّكَ مَيِّتٞ وَإِنَّهُم
مَّيِّتُونَ ٣٠ ثُمَّ إِنَّكُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ عِندَ رَبِّكُمۡ تَخۡتَصِمُونَ ٣١



(22) Yanzu wanda Allah ya yalwata qirjinsa da musulunci, ya shiryu zuwa gare shi, kuma yana kan basira daga Ubangijinsa, kamar misalin wanda zuciyarsa ta qeqashe ne daga barin ambaton Allah?. Ba zasu yi daidai ba har abada. Shiryayyu ne zasu tsira, tavewa kuwa ta tabbata ga waxanda zukatansu suka qeqashe daga ambaton Allah. Waxannan suna cikin vata daga barin gaskiya mabayyani. (23) Allah ya saukar da Alqur'ani ga Manzonsa Muhammad (S.A.W) wanda shi ne mafi kyan zance. Ya saukar da shi mai kama da juna, sashensa yana kama da sashe, wajen gaskiya da kyau da haxuwa, da rashin savawa, cikinsa akwai labarai da hukunce-hukunce kala-kala, da alqawarin ni'ima da alqawarin azaba, da siffofin masu gaskiya, da siffofin mavarnata, da sauransu. Fatun jikin waxanda suke tsoron Ubangijinsu suna tashi yayin da suka ji abin da yake cikin Alqur'ani da alqawarin narkon azaba da tsoratarwa, sannan sai zukatansu da fatunsu su yi laushi zuwa ga ambaton Allah, yayin da suka ji abin da yake cikinsa na busharori. Wannan abin da aka ambata na Alqur'ani da tasirinsa shiriyar Allah ce, yana shiryar da wanda ya ga dama da ita, duk wanda Allah ya tavar, bai datar da shi zuwa ga shiriya ba, to babu wani mai shiriya da zai shiryar da shi. (24) Yanzu wannan da Allah ya shiryar da shi, kuma ya datar da shi a duniya, kuma ya shigar da shi Aljannah a lahira, zai daidaita da wanda ya kafirta kuma ya mutu a kan kafircinsa, Allah ya shigar dashi wuta, hannunsa da qafafuwansa a xaure, ba zai iya kare kansa daga wannan wuta ba sai da fuskarsa da yake kife a kanta?. Za a cewa waxanda suka zalunci kansu da kafirci da savo a yanayi na izgili: "Ku xanxani abin da kuka kasance kuna aikatawa na kafirci da savon Allah, wannan shi ne sakamakonku. (25) Al'ummun da suka kasance gabanin waxannan mushirikai sun qaryata, sai azaba ta shammace su ta inda basa jin zata zo, ballantana ma su yi mata danadi da tuba. (26) Sai Allah ya xanxana musu qasqanci da kunyata tun a nan duniya da wannan azaba, kuma tabbas azabar lahira da take jiran su tafi ta duniya tsanani, da a ce sun san hakan. (27) Kuma haqiqa mun bugawa mutane misalai daban-daban na alheri da sharri, da gaskiya da vata, da Imani da kafirci da sauransu, a cikin wannan alqur'ani da aka saukarwa Annabi Muhammad (S.A.W) domin kwaxayin ko zasu yi izina da misalan, su yi aiki da gaskiya, su qyale vata.

(28) Mun sanya shi Alqu'ani da harshen larabci, babu karkacewa ko sarqaqiya a cikinsa, don kwaxayin ko sa ji tsoron Allah ta hanyar aiki da umarninsa, da kuma hanuwa ga haninsa.

(29) Allah ya buga misalin mushiriki da mai kaxaita Allah da wani mutum bawa da wasu abokan tarayya masu jayayya a kansa suka mallaka, idan ya farantawa wani sai ya zama ya munanawa wani, don haka yana cikin ruxani da tararrabi. Kuma ya buga misali da mutumin da mai mallakarsa mutum xaya ne, shi kaxai ne yake mallakarsa, kuma ya san me yake so, don haka yana cikin nutsuwa da kwanciyar hankali, ka ga waxannan bayi guda biyu ba zasu tava zamowa xaya ba. Godiya ta tabbata ga Allah, sai dai da yawansu basu sani ba, don haka suke yin tarayya da Allah. (30) Tabbas kai wannan Manzon sai ka mutu, kuma su ma sai sun mutu, ba makawa.

(31) Sannan tabbas - Ya ku mutane - a ranar alqiyama a gaban Ubangijinku zaku yi jayayya game da abin da kuka yi savani a tsakaninku, sai mai gaskiya ya bayyana daga maras gaskiya.

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

1 - Ma'abota imani da taqawa su ne waxanda suke jin tsoron Allah yayin da suka ji Alqur'ani. Ma'abota savon Allah da tavewa su ne waxanda basa amfanuwa da Alqur'ani. 2 - Qaryata saqon da Manzanni suka zo da shi shi ne sababin da yake janyo azabar Allah, ko a duniya ko a lahira, ko a duka biyun. 3 - Alqur'ani bai bar wani lamari na duniya ko lahira ba sai da ya bayyana shi, ko dai a dunqule ko a fayyace, kuma ya buga misalai a kansa.